# NAU'IKAN

# ZIKIRIN SALLA

DR. ABUBAKAR MUHAMMAD ISA

Haƙƙin Mallaka (HM): Cibiyar Fassara ta Ar-Rahyan (2025)
GSM: 08036223067
Whatsapp: 07049325138
*Email: abuamatullahi83@gmail.com*

Tunasarwa:
Ba a yarda a buga ko a kwafi wani ɓangare na wannan littafi don yin amfani da shi ta kowace irin hanya ba, ba tare da izini daga marubuci ko Cibiyar Fassara ta  Ar-Rayhan ba.

An Fara Bugawa a Shekarar: 1447 = 2025

ISBN: 978-978-697-841-3.

Maɗabba'a:
Iconic Computer and Printing Services.
08033676155.

## Gabatarwa

Haƙiƙa addinin Musulunci addini ne da Allah ya yarda da shi, kuma ba ya karɓar wani addini idan ba shi ba. Duk wanda ya zo da wani addini a ranar alƙiyama ba na Musulunci ba; Allah ba zai karɓe shi ba, kuma yana daga cikin asararru.

Kowanne ɓangare a cikin ɓangarorin addini, idan aka yi nazari mai zurfi a kansa, za a fahimci akwai salo na sauƙi da nishaɗi da wayewa. Idan muka ɗauki ɓangaren da ya shafi mafi girman ibada; watau Sallah, za mu samu tana cike da irin wannan kyakkyawan tsarin na Musulunci na samar da nishaɗi a cikinta.

Haka abin da ya shafi addu'o'in da ake yi a cikin Sallah da wajenta, tana cike da banƙaye wajen nau'o'ikan da aka shara'anta na addu'o'i; ta yadda musulmi zai samu cikaccen nishaɗi wajen yin mabambantan addu'o'i.

Littafin "Attanwi'i Fi Azkaris Salati" na babban malami Ɗariƙ ɗan Muhammad Alƙaɗɗani, littafi ne wanda ni ban ga littafin da ya tattaro nau'ikan addu'o'in Sallah a ilimance bisa tsari mai kyau, kuma a taƙaice kamar shi ba; sai dai ya rubuta shi ne da harshen Larabci, sai naga kyawun fassara shi da harshen Hausa, bisa gudummawar wani bawan Allah wanda ya ɗauki nauyin buga littafin. Haƙiƙa hakan zai taimaka wajen matso da ilimi kusa domin samun cikacciyar

amfanuwarsa ga waɗanda suke iya karanta Hausa a faɗin duniya.
Wasu daga cikin muhimman abubuwan da yakamata mai karanta wannan littafi ya sani sun haɗa da;
Na samu fassarar irin wannan littafi wanda Dr. Imam Muhammad Tukur Adam Al-manar, wanda aka buga a shekarar 2024, sai dai ta sa fasarar ta samu naƙasu ta ɓangarori kamar haka:
Na Farko Rashin lazimtar ƙa'idojin rubutun Hausa a wasu ɓangarorin.
Na Biyu: Kuskuren fassara wasu gurare kamar yadda yake a littafin: "Ya Allah ka tsaftaceni daga kusa-kuraina, kamar yadda ka tsaftace farin tufafi daga datti, Ya Allah ka wankeni daga kusa-kuraina da ruwa da ƙananan ƙanƙara da manyan ƙanƙara", daga shafi na 12, zuwa 13.
Na Uku: Bai kawo zikiri ko ɗaya da Larabci ba! Wanda hakan zai zamo naƙasu, ga karanta zikirin yadda ya kamata.
Na Huɗu: Littafin bai samu bitar malamai da nazarin su ba (Taƙrizi).
Na Biyar: Rashin daidaitaciyar Hausa a mafi yawan gurare kamar " fusfura" a maimakon furfura, a shafi na 40, da "kusa-kura", maimakon kurakurai, da "chanchanta", a shafi na 24 maimakon cancanta, da abinda a shafi na 24, maimakon abin da, da "aminchin Allah" a shafi na 34 maimakon amincin Allah.

Ina roƙon Allah ya karɓa masa daidansa, ya gafarta masa kurakuransa, tare da mu gabaɗaya.
Allah ya sakawa marubucin littafin da wanda ya ba da gudummawa ta dukkanin kayan aikin tarjama da sauransu, Dr Abubakar Muhammad Abubakar, (Daraktan Alfurƙan Kano, Nigeria), ta hannun malam Salisu Ahmad Imam. Allah kaɗai nake roƙo da ya karɓi wannan aiki ya sa a mizanin ladanmu ya kuma amfanar da al'umar Musulmai bakiɗaya.

Dr. Abubukar Muhammad Isa

# Godiya

Dukkan yabo da cikacciyar godiya mara iyaka ta tabbata ga Mahalicci mai ni'imomi marasa iyaka. Tsira da amincin Allah su ƙara tabbata ga fiyayyan halitta, mafi cancantar a gode masa a cikin halittu Annabi Muhammad shugaban Annabawa da Manzanni.

Ina godiya ga iyaye da malamai, da dukkanin waɗanda aka haɗu a cikin ayyukan alheri. Dole na keɓance godiya ga bawan Allan da koyaushe ya bar min ƙofarsa a buɗe, domin taimakawa wajen yaɗuwar ilimi mai amfani da aiki da shi, haka kuma ina gode wa, Daraktan cibiyar Alfurƙan Dr. Abubakar Muhammad Abubakar. Godiyar ba za ta cika ba, sai na keɓanci godiya da jinjina da yabawa ga malaman da suka tsaya wajen bayar da kyawawan shawarwari, da kuma sanya albarkar wani sashensu, kamar: Dr. Aliyu Yunus Muhammad (Babban limamin masallacin Usman bin Affan Gadon Kaya, Kano Nigeria), da Dr. Jibril Ɗalhat (Babban limamin sabon masallacin Juma'a Rafin-guza Kawo Kaduna, Nigeria), da Dr. Auwal Yusuf Khidir, (Wakilin makaranta Kwaru), malami a jami'ar Kaduna. Da kuma Babban limamin masallacin Juma'a na A.R.T.V Kano, kuma malami a sashen nazarin kimiyar na'ura mai ƙwaƙwalwa a jami'ar Northwest Kano, saboda cikacciyar gudummawarsa da tsayuwarsa, wajen Ingantuwar aikin, Sheikh Sukairaj Hafiz Imam. Da kuma Farfesa Yahaya

Mujahid daga jami'ar Ahmadu Bello Zariya, da Farfesa Hafiz Yusuf Imam, daga jami'ar Bayero( Sarkin yaƙin Makaman Kano), saboda kulawar da ya bayar, wajen bitar littafin gabaɗaya, da ba da kyawawan shawarwari, da Dr Nura Baba Yakasai daga Sa'adatu Rimi College of Education Kano, da kuma Dr Aminu Salisu babban malami a AKCILS Kano, da kuma ɗalibi mai albarka kuma malami Nafiu Sabiu Ahmad Mariri, Saboda rashin ƙosawarsa da jajircewarsa a kowanne lokaci aka buƙaci aikin da zai iya na inganta harkokin fassara littafi da wallafa. Da kuma kwamitin bibiya da tabbata da saituwar littafi ƙarƙashin jagorancin Chief editor Dr. Nuraddeen Ado Gezawa da Malam Nafiu Sabiu Ahmad Mariri, da malam Ahmad Aminu Nuhu.
A ƙarshe ina gode wa dukkanin waɗanda suka ba da gudummawa a fili-da-ɓoye, ta iliminsu ko dukiyarsu, ko lokacinsu, Allah ya saka wa kowa da mafificin sakamako a duniya da lahira, ya karɓi wannan aiki a gurinsa, sannan ya sanya shi karɓaɓɓe a duniyar Musulunci.

Dr. Abubakar Muhammad Isa

GABATARWAR DR. ALIYU YUNUS MUHAMMAD

Taƙrizi

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah, tsira da amincin sa su tabbata ga fiyayyen halitta Annabi Muhammad (s.a.w) da alayensa masu daraja da sahabbansa masu girma da waɗanda suka bi hanyarsu har ranar alkiyama.

Bayan haka salla ita ce mafificiyar ibada a cikin dukkan ibadoji wacce Annabi (S.A.W) yace ita ce farkon abinda za,a yiwa bawa hisabi akanta a gobe kiyama. Dukkan musulmi nagari yana ƙoƙarin yaga ya inganta sallarsa wajen kiyaye sharaɗanta da farillanta da sunnoninta, daga cikin muhimman al'amura a cikin sallah shi ne addu’a da Manzon Allah (s.a.w) ya koyar. Ya kamata a ce dukkanin musulmi ya koyi addu’o’in da ake yi a cikin sallah don ya riƙa yi. To ga wani karin littafin cikin jerin littatafai da ɗan uwanmu Dr Abubakar Muhammad Isa ya fitar don amfanar da al,ummar musulmi. Wannan littafi fassara ne na wani littafin addu’o’i mai matuƙar amfani wanda yake ɗauke da addu'o’in da ake karantawa a cikin sallah. Dr. Abubakar ya fassara shi cikin harshe Hausa don mai karantawa ya san fassarar abinda yake karantawa .

Tabbas, mu musulmi al-umma ce ta karatu, muna bukatar a samu wasu daga cikin mu su daure wajen wallafe wallafe musamman a harshen mu na Hausa don kwaɗaitarwa al-

umma wajen karatu a zamanin da kafofin sada zumunta suka ɗauke hankalin mafi yawan mutane.
Allah ya sakawa wannan ɗan'uwa da alheri, ya sa wannan aiki a mizanin ayyukan sa na alheri. Allah ya ƙaro mana mutane masu himma irinsa.

**Aliyu Yunus Muhammad,**
Limami a masallacin Usman Bn Affan Gadon Kaya, Kano.
Kuma,
Mai Karantarwa a Jami'ar Horon Malamai,
(Maitama Sule University of Education) Kano.
27 Muharram 1447H- 22 July 2025 CE

# GABATARWAR DR. JIBRIL ƊALHAT

## بسم الله والصلاة والسلام على رسول الله وعلى آله وصحبه ومن تبعهم بإحسان إلى يوم الدين

Bayan na samu damar karanta wannan littafi na fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan littafi zai ba wa mutane da yawa waɗanda basu iya karatun Larabci ba damar fahimtar addininsu.
2. Wannan littafi ya kawo wa mai karatu nau'i daban-daban daga cikin addu'o'i da Manzon Allah (S. A. W), yake yi a wurare mabambanta a cikin salla wanda duk wanda mutum ya zaɓa ya yi sallarsa ta yi.
3. Haka kuma wannan littafi ya kawo wa mai karatu nau'ika daban-daban na ayyukan Manzon Allah (S.A.W), a wasu wuraren salla wanda kuma duk wanda mutum ya yi sallarsa ta yi.
4. Al'amarin bai tsaya nan ba, littafin ya ƙunshi wasu salo da za su taimaka wa mai karatu ya inganta sallar shi don ya samu cikakken lada kamar: ƙasƙantar da kai; daidaituwa; da kuma tsoron Allah a cikin salla.

Don haka ina mai ƙarfafa wa mutane gwiwa don mallakar wannan littafi da karanta shi, tare da aiki da shi.

Allah (S.W.A) ya sanya wa wannan littafi albarka ya kuma ƙara wa Dr. Abubakar Muhammad Isa lafiya da basira da ƙwarin gwiwa wajen hidimta wa addini ya kuma haɗamu a ladan gabaɗaya.

**Dr. Jibril Ɗalhat,**
Imam Sabon Masallacin Jumu'a Rafin Guza Kawo Kaduna.
Hukumar kula da harshen Larabci da addinin Musulunci ta ƙasa (NBAIS).

## GABATARWAR DR. AWWAL YUSUF KHIDIR

## بسم الله الرحمن الرحيم

Ina farawa da sunan Allah Mai rahama Mai jin ƙai, ina salati ga Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare Shi da Alayensa, da Sahabbansa bakiɗaya, Amin.

Bayan Haka, na karanta wannan littafi wato fassarar littafin "Attanwi'i Fi Azkaris Salati" na babban Malami Ɗariƙ ɗan Muhammad Alƙahɗani daga harshen Larabci zuwa Hausa wanda Dr. Abubakar Muhammad Isa ya fassara.

Haƙiƙa wannan aiki da Dr. Abubakar yayi na fassara wannan littafi zuwa harshen Hausa gagarumin aiki ne wanda ya cancanci jinjina da yabo saboda alaƙar aikin da Sallah bugu da ƙari zai ƙara kusanto da ilimin sanin nau'oin zikirorin sallah kusa da al'umma duba da yanayin da muke ciki na ƙishirwar ilmin sallah.

Kuma wani abin ban sha'awa shi ne yadda Dr. Abubakar tsara aikin kuma ya yi amfani da daidaitacciyar Hausa tare da kula da ƙa'idojin fassara wajen fassara wannan littafi wanda hakan zai ba da dama ga duk mai fahimtar harshen Hausa ya iya karantawa da kuma fahimtar abin da littafin ya ƙunsa ,

A karshe ina Addu'ar Allah ya saka wa Dr. Abubakar da mafificin alkhairi, Allah ya karɓi aikin a matsayin sadaka mai gudana, da wannan nake jawo hankalin al'umma, hukumomi, ƙungiyoyi da masu hannu-da-shuni da mu sanya hannu wajen bugawa da yaɗa wannan muhimmin alkhairi don muyi tarayya wajen wannan gagarumin aiki na yaɗa addini.

**Dr. Auwal Yusuf Khidir,**
(Wakilin Makaranta Kwaru)
Department of Arabic, Faculty of Arts
Kaduna State University, Kaduna.

## GABATARWAR MALAM SUKAIRAJ HAFIZ IMAM

Littafin Nau'ikan Zikirai wanda dan uwa Dr. Abubakar Muhammad Isa ya rubuta wata muhimmiyar fassara ce daga harshen Larabci zuwa Hausa da ke bayani dalla-dalla kan zikiri da addu'o'in da Manzon Allah ﷺ ke karantawa a cikin sallah . Littafin ya rarraba zikiri bisa tsari da lokaci: daga lokacin shiga sallah da kabbarar harama, zuwa addu'ar fara sallah, karatun Al-Kur'ani, ruku'u, sujjada, tahiya, har zuwa sallama da zikiri bayan salla. Hakanan, ya haɗa da addu'o'in da ake karantawa a sallolin dare, nafiloli da sallolin musamman kamar idi da jumu'a. Wannan tsari yana sauƙaƙa wa mai karatu fahimtar yadda ake kyautata ibada bisa koyarwar sunnah, kuma yana taimakawa wajen ilmantar da Musulmi da ke karanta Hausa, su fahimci hanyoyin da za su bi wajen gudanar da sallah kamar yadda Manzon Allah ﷺ ya koyar.

Bugu da ƙari, littafin ya zurfafa cikin bayanin yadda sahabbai da magabata ke gudanar da sallah da nutsuwa da tsoron Allah. Yana bayyana matsayin "khushu'i" (wato ƙanƙan da kai da jin tsoron Allah a cikin zuciya yayin ibada) da yadda hakan ke tasiri wajen karɓar sallah. Littafin ya kawo misalan rayuwar sahabbai kamar Sayyidina Umar, Ibn Mas'ud, Abdullahi Ibn Zubair, da magabata irin su Hasanul Basari da Sufyan Ath-Thawri, wadanda suka bambanta da musulmai a zamanin yau wajen nutsuwa da kyautata sallah. Wannan ɓangare yana da mahimmanci domin yana koyi da kwaɗaitar da mai karatu ya ɗauki sallah da muhimmanci tare da fahimtar cewa bautar Allah ba kawai ta jiki ba ce, har da zuciya da girmamawa da tsarkake niyya.

A ƙarshe, littafin ya ƙarfafa muhimmancin sallah a cikin jama'a da fa'idar tsayar da sallar farilla guda biyar a lokaci. An kawo dalilai daga Al-Kur'ani, hadisan Manzon Allah ﷺ da kalaman sahabbai da ke nuna wajabcin zuwa masallaci da muhimmancin kasancewa cikin jam'i. Littafin ya kuma yi bayani kan falaloli da sakamakon sallah kamar yadda hadisi ya tabbatar da cewa sallah tana goge ƙananan zunubai kuma ita ce abin farko da za a fara tambaya akai a ranar Alƙiyama. Hakanan, ya kawo hanyoyin da za su taimaka wa Musulmi ya samu khushu'u a cikin sallah, kamar fahimtar ma'anar ayoyin da ake karantawa, nisantar shagala da duniya, da rayuwa cikin tsoron Allah da biyayya. A taƙaice, littafin Nau'ikan Zikirai jagora ne mai zurfi da amfani wajen ƙarfafar musulmi su gyara ibadarsu da dangantakarsu da Ubangiji.

Sukairaj Hafiz Imam,
Limamin Masallacin Juma'a na ARTV.
Malami a sashin nazarin kimiyar na'ura mai ƙwaƙwalwa,
Jami'ar Northwest, Kano.

## GABATARWAR DR. AMINU SALISU

### Shimfiɗa (Taƙriz)

*Bismillahir rahmanir rahim*

Dukkan yabo sun tabbata ga Allah Ubangiji maɗaukaki, Tsira da aminci su tabbata ga fiyayyan halitta, Annabi Sallallahu alaihi Wasallama.

Muna ƙara godiya ga Allah bisa tagomashi da yake mana da zaratan matasan Malamai irin su Dr Abubakar Muhammad Isa wanda ya sadaukar da rayuwarsa, wajen kusanto wa da al'umma abin da zai amfane ta na addini a duniya da lahira. Daga cikin irin wannan tagomashi shi ne: fassara da ya yi wa littafi mai suna 'Nau'ikan zikiran Salla' Haƙika Dr ya yi ƙoƙarin fassara wannan littafin cikin harshen Hausa don kusanto wa da al'umma bayanai a sauƙaƙe kuma gamsashshe kan salo daban-daban na zikirai da ake yi a salla. Ya fara fassara zikirai tun daga fara salla har zuwa kammalawa. Ba a nan ya tsaya ba hatta wasu nau'o'in zikirai da ake a wasu sallolin nafila kamar shafa'i da wuturi da raka'o'i biyu na alfijir ya ambato su. Muna fatan ƴan'uwa za su karanta wannan littafin da idon basira domin ƙara kyautata sallarsu wadda ita ce ginshikin addininsu.

Muna fatan Allah ya amfanar da mu ya ba mu ikon yin aiki da abin da muka karanta, Shi kuma Dr Abubakar Muhammad Isa Allah ya saka masa da alkhairi ya albarkaci zuriyarsa.

**Dr. Aminu Salisu ,**
Department of Islamic Studies,
AKCILS, Kano.

# kunshiya


| | Shafi |
|---|---|
| Gabatarwa | iii |
| Godiya | vi |
| Gabatarwar Dr. Aliyu Yunus Muhammad | viii |
| Gabatarwar Dr. Jibril Ɗalhat | x |
| Gabatarwar Dr. Awwal Yusuf Khidir | xi |
| Gabatarwar Sukairaj Hafiz Imam | xii |
| Gabatarwar Dr. Aminu Salisu | xiv |
| **Abubuwan Dake Ciki** | xv |

**FASALI NA FARKO:**

| | |
|---|---|
| **Nau'ikan Zikiran Sallah** | **1- 25** |
| Kabbarar Harama | 2 |
| Karatun Ma'aiki (S.A.W) | 5 |
| Addu'o'i Yayin Ruku'u | 14 |
| Addu'o'in Sujjada | 16 |
| Addu'o'in Sallar Dare | 17 |
| Sigogin Tahiya | 18 |
| Sigogin Salatul Ibrahimiyya | 20 |
| Sallama | 23 |
| Addu'o'i Bayan Idar Da Salla | 24 |

FASALI NA BIYU:


| | |
|---|---|
| Wasu Daga Cikin Hukunce-Hukuncen Salla | 26 - 62 |
| Jin Tsoron Allah a Cikin Salla | 27 |
| Halayen Masu Tsoron Allah a Cikin Sallah | 30 |
| Samuwar Tsoron Allah a Cikin Salla | 35 |
| Kwaɗaitarwa Cikin Al'Amuran Salla | 38 |
| Kwaɗaitarwar Tsayar Da Sallolin Farilla | 40 |
| Wajabcin Salla a Cikin Jama'a | 43 |
| Tambayoyin Wajabcin Salla Cikin Jama'a | 50 |
| Sallar Mutum Ɗaya a Bayan Sahu | 51 |
| Hukuncin Wanda Ya Bar Salla | 52 |
| Siffofin Sallar Ma'Aiki (S.A.W) | 56 |
| Addu'o'i Bayan Idar Da Sallah | 58 |
| Tambayoyi Masu Muhimmanci | 59 |

| | |
|---|---|
| Kammalawa | 63 |
| Wasu Cikin Litattfan Marubucin | 64 |

# FASALI NA FARKO

## NAU'IKAN ZIKIRAN SALLAH

## KABBARAR HARAMA

Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana buɗe sallarsa da faɗin “Allahu Akbar”[1] wato Allah shi ne mai girma.

- ❖ Ya kasance yana ɗaga hannayensa tare da kabbara.[2]
- ❖ Wani kuma yana ɗaga hannayen bayan ya yi kabbara.[3]
- ❖ Wani lokacin sai ya ɗaga hannayen sannan ya yi kabbarar.[4]
- ❖ Ya kasance yana sanya hannayensa kusa da kafaɗunsa.[5]
- ❖ Wani lokacin yakan ɗaga hannayen har ya kusantar da su dab da kunnuwansa[6]

## Addu’ar Fara Salla

Ma’aiki ya kasance yana karanta addu’o’i daban daban, wani lokacin ya karanta wannan wani lokacin kuma waccan, kamar:

**«اللَّهُمَّ بَاعِدْ بَيْنِي وَبَيْنَ خَطَايَايَ كَمَا بَاعَدْتَ بَيْنَ الْمَشْرِقِ وَالْمَغْرِبِ، اللَّهُمَّ نَقِّنِي مِنَ الْخَطَايَا كَمَا يُنَقَّى الثَّوْبُ الأَبْيَضُ مِنَ الدَّنَسِ، اللَّهُمَّ اغْسِلْنِي مِنْ خَطَايَايَ بِالْمَاءِ وَالْبَرَدِ وَالثَّلْجِ» .**

---

1 Muslim
2 Bukhari da Nasa'i
3 Bukhari da Nasa'i
4 Bukhari da Abu Dawud
5 Bukhari da Nasa'i
6 Bukhari da Abu Dawud

- "*Ya Ubangiji! Ka nesanta tsakanina da kurakuraina kamar yadda ka nesanta mahudar rana da mafaɗarta. Ya Ubangiji! Ka tsaftace ni daga kurakuraina kamar yadda ake tsaftace farar tufa daga datti. Ya Ubangiji ka wanke ni daga kurakuraina da ruwa da ƙanƙara da kuma sanyi*".[7]

- "Na juyar da fuskanta ga wanda ya ƙagi halittar sammai da ƙasa ina mai ƙyale dukkan karkatattun addinai, ina mai miƙa wuya ga Allah kuma bana daga cikin masu shirka. Lallai sallata da yankana da rayuwata da mutuwata ga Allah kaɗai Ubangijin halitttu suke, ba shi da abokin tarayya, da wannan aka umarce ni, kuma ni ne farkon masu miƙa wuya. Ya Ubangijj! Kai ne Sarkin sarakuna, babu abin bauta bisa cancanta sai Kai, tsarki ya tabbata gare ka, haka ma godiya, kai ne Ubanigina, ni bawan ka ne, na zalinci kaina, ina mai tabbatar da zunubaina, ka gafarta mini su gabaɗaya, lallai babu mai gafarta zunubai sai kai, ka shiryar da ni zuwa ga kyawawan ɗabi'u domin babu mai shiryarwa zuwa ga kyawawan ɗabi'u sai Kai, Ka kautar mini da munanansu domin babu mai kawar da munanansu sai Kai, ina mai amsa maka, ina mai neman dacewa a wajen ka, dukkan alheri daga wajen ka yake, duk wani sharri ba ya zuwa daga gare ka, shiryayye shi

[7] Bukhari da Muslim

ne wanda aka shiryar, ni naka ne, kuma zuwa gare ka nake, babu matsera kuma babu mafaka daga gareka sai zuwa gare ka, albarkatunka sun yawaita, ka ɗaukaka, ina neman gafararka, ina mai tuba zuwa gare ka".[8]

❖ "*Tsarki ya tabbata gare ka Ya Ubangijj, da gode maka, albarkar sunanka ya yawaita, matsayinka ya ɗaukaka, babu abin bauta bisa cancanta koma bayanka*".[9]

: «سُبْحَانَكَ اللَّهُمَّ وَبِحَمْدِكَ، وَتَبَارَكَ اسْمُكَ، وَتَعَالَى جَدُّكَ، وَلاَ إِلَهَ غَيْرُكَ» .

❖ "Allah kai ne mafi girman masu girma, abin yi wa godiya mai yawa, abin tsarkakewa a safiya da yammaci".[10]

❖ "Yabo da godiya masu yawa sun tabbata ga Allah masu ɗaɗi kuma da albarka a cikinsa"

Wasu daga cikin addu'o'in da Ma'aiki tsira da amicin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake yi a sallar dare:

❖ "Ya Allah! Ubangijin Jibriliu da Mika'ilu da Israfilu, maƙagin sammai da ƙasa, masanin abin da ya ɓuya da abin da ya bayyana, kai ne za ka yi hukunci a tsakanin bayinka cikin abin da suka kasance suna saɓawa, Ka shiryar da ni cikin abin da suka saɓa na gaskiya a bisa

---

[8] Muslim da Abu Dawud
[9] Abu Dawud Hakim
[10] Muslim

izinin ka domin lallai kai ne mai shiryarwa zuwa ga hanya miƙaƙƙiya".[11]

- ❖ "Ma'aiki ya kasance yana faɗin "Allahu Akbar" sau goma, "Alhamdulillahi" sau goma, "Subhanallahi" sau goma, "La'ilaha illa lahu" sau goma, "Astagfirullaha" sau goma, sannan ya ce: "Ya Ubangijj! Ka gafarta mini, Ka shiryar da ni, Ka azurta ni, Ka bani lafiya" sau goma, sannan ya ce: "Ya Ubangiji! Ina neman tsarinka daga ƙunci ranar hisabi" sau goma"[12]
- ❖ "Allahu Akbar" sau uku, "Ma'abocin Mulki da ƙasaitar Mulki da Cikakken girma da ɗaukaka".

## Karatun Ma'aiki (S.A.W)Tsira da Amincin Allah Su Kara Tabbata a Gare Shi

### Sunnatul Fajr

- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana gajarta karatu ƙwarai da gaske a sallar sunnatul Fajr har Nana Aisha Allah ya ƙara mata yadda ta kasance tana cewa: "Shin ya karanta Fatiha ma kuwa".[13]

Ya kasance a wasu lokutan yana karanta Fatiha a raka'ar farko da kuma:

---

[11] Muslim
[12] Ahmad da Ɗabarani
[13] Bukhari da Muslim

(قُولُوا آمَنَّا بِاللَّهِ وَما أُنْزِلَ إِلَيْنا وَما أُنْزِلَ إِلى إِبْراهِيمَ وَإِسْماعِيلَ وَإِسْحاقَ وَيَعْقُوبَ وَالْأَسْباطِ وَما أُوتِيَ مُوسى وَعِيسى وَما أُوتِيَ النَّبِيُّونَ مِنْ رَبِّهِمْ لا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِنْهُمْ وَنَحْنُ لَهُ مُسْلِمُونَ).[14]

A raka'a ta biyu bayan Fatiha yana karanta:

قُلْ آمَنَّا بِاللَّهِ وَما أُنْزِلَ عَلَيْنا وَما أُنْزِلَ عَلى إِبْراهِيمَ وَإِسْماعِيلَ وَإِسْحاقَ وَيَعْقُوبَ وَالْأَسْباطِ وَما أُوتِيَ مُوسى وَعِيسى وَالنَّبِيُّونَ مِنْ رَبِّهِمْ لا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِنْهُمْ وَنَحْنُ لَهُ مُسْلِمُونَ)[15]

Wani lokacin kuma yana karanta:

فَلَمَّا أَحَسَّ عِيسى مِنْهُمُ الْكُفْرَ قالَ مَنْ أَنْصارِي إِلَى اللَّهِ قالَ الْحَوارِيُّونَ نَحْنُ أَنْصارُ اللَّهِ آمَنَّا بِاللَّهِ وَاشْهَدْ بِأَنَّا مُسْلِمُونَ)[16]

A duk raka'o'i biyun madadin ayoyin da suka gabata.

Wani lokacin a raka'a ta farko bayan Fatiha yana karanta:

قُلْ يا أَيُّهَا الْكافِرُونَ (١) لا أَعْبُدُ مَا تَعْبُدُونَ (٢) وَلا أَنْتُمْ عابِدُونَ مَا أَعْبُدُ (٣) وَلا أَنا عابِدٌ مَا عَبَدْتُّمْ (٤) وَلا أَنْتُمْ عابِدُونَ مَا أَعْبُدُ (٥) لَكُمْ دِينُكُمْ وَلِيَ دِينِ (٦)[17]

A Raka'a ta biyu bayan Fatiha yana karanta:

---

[14] Suratu Al Imran 136

[15] Suratul Baƙara 84

[16] Suratu Al Imran 52

[17] Suratul Kafirun 1- 6

Ya kasance yana cewa madallah da waɗannan surori guda biyu:

قُلْ هُوَ اللهُ أَحَدٌ (١) اللهُ الصَّمَدُ (٢) لَمْ يَلِدْ وَلَمْ يُولَدْ (٣) وَلَمْ يَكُنْ لَهُ كُفُواً أَحَدٌ (٤) [18]

## Sallar Asuba

- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta suratul Waƙi'a ko Aɗɗur ko Attakwir ko Rum ko Yasin ko Assaffat ko Almuminun ko Sajda ko Al,insan ko Zalzala ko kuma ya karanta daga cikin surorin da ake kiransu "Ɗiwalul Mufassil".[19]
- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana tsawaita karatu a raka'ar farko, ya taƙaita wa a raka'a ta biyu. Ya kasance yana karanta kwatankwacin ayoyi 60 zuwa sama, wasu daga cikin waɗanda suka rawaito Hadisin sun ce zai iya zama a raka'ar ko a duk biyun.[20]
- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya karanta "Suratul Zalzala" a raka'o'i biyun duka har marawaicin Hadisin ya ce: "Ban sani ba Ma'aiki ya manta ne ko yana sane ya maimaita surar".

---

[18] Suratul Ikhlas 1- 4
[19] Daga suratu "Kaf" zuwa "Naba'i
[20] Bukhari da Muslim

## Sallolin Azahar Da La'asar

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta gwargwadon aya 30 a raka'a biyun farko, a wasu lokutan ya kasance yana karanta Ɗarik da suratul Buruj da suratul Lail da kuma makamantansu.[21]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana tsawaitawa a raka'ar farko fiye da raka'a ta biyu.[22]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana tsawaita karatu a sallar Azahar gwargwadon aya 30 a raka'a biyun farko, a raka biyun ƙarshe kuma gwargwadon rabin raka'a'i biyun farko. A wasu lokutan Fatiha kaɗai yake karantawa.[23]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance a raka'o'i biyun farko na sallar La'asar yana karanta gwargwadon ayoyi 15 a raka'o'in biyun ƙarshe kuma yana taƙaitawa ƙasa da raka'o'i biyun farko ko gwargwadon rabin abin da ya karanta a raka'o'i biyun farko.[24]

---

[21] Abu Dawud
[22] Bukhari da Muslim
[23] Muslim
[24] Muslim

## Sallar Magriba

- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta gajerun surori a wasu lokutan[25]. A wasu lokutan kuma yana karanata "Ɗiwalul Mufassal" ko "Ausaɗuhu"… A wasu lokutan kuma yana karanta suratuɗ-ɗuri da suratul Mursalati da suratul A'araf[26] A wasu lokutan kuma suratul Anfal.[27]
- ❖ Wata rana a halin tafiya Ma'aiki sai ya karanta suratut-tini a raka'a ta biyu.[28]

## Nafilar Bayan Sallar Magriba

- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta suratul Kafirun a raka'ar farko, a raka'a ta biyu kuma ya karanta suratul Ikhlas.[29]

## Sallar Isha'i

- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karantawa a raka'o'i biyun farko surorin da ake kira "Wasaɗul Mufassal".[30]

---

[25] Bukhari
[26] Bukhari
[27] Ɗabarani
[28] Ahmad
[29] Nasa'i
[30] Ahmad

- A wani lokacin yana karanta suratush-shams da ire-irenta.[31]
- Wani lokacin kuma yana karanta sutaul Inshiƙaƙ( إِذَا السَّمَاءُ انْشَقَّتْ)[32], kuma ya kasance yana yin sujjadar Tilawa a (cikin Surar inda  ayar tazo).[33]

**( وَإِذا قُرِئَ عَلَيْهِمُ الْقُرْآنُ لا يَسْجُدُونَ)**[34]

A halin tafiya ya karanta suratut Tini a raka'ar farko.[35]

## Sallar Dare

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance a wasu lokutan yana bayyana karatu, a wasu lokutan kuma yana ɓoyewa.[36]
- Wasu lokutan ya tsawaita karatu, wani lokacin kuma ya taƙaita, wani lokacin yana kaiwa matuƙa wajen tsawaita karatu har Abdullahi ɗan Mas'ud ya ce: "Wata rana na yi sallar dare tare da Ma'aiki, bai gushe ba yana tsaye har sai da na himmatu na aikata ba daidai ba. Aka ce masa, me kaso ka aikata? Ya ce: Na himmatu na zauna na ƙyale Ma'aiki shi kaɗai".[37] Duk wannan saboda yadda yake tsawaitawa.

---

[31] Ahmad
[32] Suratul Inshiƙaƙ 1
[33] Bukhari
[34] Suratul Inshiƙaƙ 21
[35] Bukhari
[36] Bukhari
[37] Bukhari

- Huzaifatu ɗan Yaman ya ce: “Na yi Sallah tare da Ma’aiki a wani dare, sai ya fara karanta suratul Baƙara. Sai na ce a zuciyata: “Zai yi Ruku’u in ya kai aya ta ɗari” sai ya wuce, na ce wataƙila zai rabata biyu ne a cikin raka’o’i biyu. Sai ya wuce, ni kuma na ce wataƙila in ya kai ƙarshe zai yi ruku’u, sannan ya fara karanta suratun Nisa’i ya karanceta gabaɗaya, Ya buɗe suratu Ali Imraan ya karanceta gabaɗaya, yana kyautata karatu (yana yinsa dalla-dalla), idan yazo kan wata aya da ta ƙunshi Tasibihi, sai ya yi. Haka, in ya wuce ta wata aya da ta ƙunshi addu’a, sai ya yi. Idan yazo kan wata aya da ta ƙunshi neman tsari; sai ya nema. Sannan sai ya yi Ruku’u”.[38]
- A wani dare ya karanta daga cikin surorin da ake kira “aɗ-ɗiwal” alhalin yana cikin rashin lafiya.[39]
- Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance a wasu lokutan yana karantawa daga cikin surorin da ake kiransu “As-Saba’uɗ -ɗiwal”.[40]
- Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance a wasu lokutan yana karanta gwargwadon aya 50 ko sama da haka, a wani lokacin yana karanta suratul Muzammil.[41]

---

[38] Muslim
[39] Hakim
[40] Abu Dawud
[41] Bukhari

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta suratul Isra'I a kowane dare, haka suratuz Zumar.[42]
- An karɓo daga Nana Aisha Allah ya ƙara mata yadda ba, ban san cewa Ma'aiki ya karance ƙur'ani gaba ɗayansa a dare ɗaya ba ko kuma ya yi tsayuwar dare tun daga farkon dare har ƙarshensa ba ko kuma ya azumci wata gabaɗayansa in ba Ramadan ba.[43]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance ba ya karance Kur'ani gaba ɗayansa a ƙasa da kwana bakwai.[44]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi bai kasance yana tsayuwar dare gabaɗayansa ba.[45]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana cewa: "Duk wanda ya yi tsayuwar dare da ayoyi goma ba za a rubuta shi daga cikin gafalallu ba. Wanda ya yi tsayuwar dare da ayoyi 100 za a rubuta shi daga cikin masu tsoron Allah. Wanda ya yi tsayuwar dare da ayoyi 1000 za a rubuta shi cikin masu tarin lada da yawa".[46]

---

[42] Ahmad
[43] Nasa'i
[44] Ibnus Sa'ad
[45] Muslim
[46] Abu Dawud

## Sallar Wutiri

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta suratul A'ala a raka'ar farko, a Raka'a ta biyu yana karanta suratul Kafirin. A raka'a ta uku yana karanta suratul Ikhlas.[47]
- Wani lokacin yana raɓa Falaƙi da Nasi bayan suratul Ikhlas.[48]
- Wata rana Ma'aiki ya karanta ayoyi 100 daga cikin suratun Nisa'i a sallar wutiri.[49]

## Sallar Juma'a

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana karanta suratul A'ala a raka'ar farko sai kuma suratul Gashiya a raka'a ta biyu.[50]
- A wasu lokutan kuma yana karanta suratul Juma'a a raka'ar farko sa'annan ya karanta suratul Munafiƙun, wani lokacin yana karanta suratul Gashiya a raka'a ta 2 maimakon suratul Munafiƙuna.[51]

## Sallolin Idi (Karama Da Babba)

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance a wasu lokutan yana karanta suratul

---

[47] Nasa'i
[48] Tirmizi da Hakim
[49] Nasa'i
[50] Muslim
[51] Muslim

A'ala a raka'a ta farko, suratul Gashiya a raka'a ta biyu. A wasu lokutan kuma suratu Kaf a raka'a ta farko, suratul Kamar a raka'a ta biyu.[52]

## Addu'o'i Yayin Ruku'u

Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana da nau'ikan addu'o'i da zikirori mabambanta, wani lokacin ya yi wannan wani lokacin ya yi wancan.

سُبْحَانَ رَبِّي الْعَظِيمَ

- "Subhana Rabbiyyal Azimi" sau uku.[53]

سُبْحَانَ رَبِّي الْعَظِيمَ وَبِحَمْدِهِ

- "Subhana Rabbiyal Azimi wa bi Hamdihi" sau uku[54]

(سُبُّوحٌ قُدُّوسٌ، رَبُّ الْمَلاَئِكَةِ وَالرُّوحِ)

- "Subbuhun Kuddusun Rabbul Mala'ikati war Ruh"[55]
- "Allahum laka Raka'atu wa bika amantu, wa laka aslamtu, anta rabbi, kasha'a laka sam'i wa basari, wa mukki, wa azami, wa asabi, wa ma saƙallat bihi ƙadami lillahi rabbil alamina".[56]

---

[52] Muslim
[53] Ahmad
[54] Abu Dawud
[55] Muslim
[56] Muslim

- ❖ “Subhanakallahuma Rabbana wa bi hamdika, Allahummagfirli”.[57]

## Daidaito Yayin Ruku’u

Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana miƙar da gadon bayansa yayin ruku’u, yana faɗin “Sami’allahu liman Hamidahu” lokacin ɗagowa daga ruku’u.[58]

Ya kasance yana addu’o’i mabanbanta yayin ɗagowa daga ruku’u:

رَبَّنَا لَكَ الْحَمْدُ

- ❖ “Rabbana lakal Hamdu”.[59]

رَبَّنَا وَلَكَ الْحَمْدُ

- ❖ “Rabbana wa lakal Hamdu”[60]

اللَّهُمَّ رَبَّنَا لَكَ الْحَمْدُ

- ❖ “Allahumma Rabbana laka Hamdu”[61]

اللَّهُمَّ رَبَّنَا وَلَكَ الْحَمْدُ

- ❖ “Allahumma Rabbana wa lakal Hamdu”[62]

A wasu lokutan yana ƙarawa da:

---

57 Bukhari
58 Bukhari da Muslim
59 Bukhari da Muslim
60 Bukhari da Muslim
61 Bukhari
62 Bukhari

**"مِلْءَ السَّمَوَاتِ وَمِلْءَ الأَرْضِ وَمِلْءَ مَا شِئْت مِنْ شَيْءٍ بَعْدُ"**

❖ "Mil'us Samawati wa Mil'ul Ardi wa Mil'u ma shi'ita min shai'in ba'adu"[63]

**"مِلْءَ السَّمَوَاتِ وَمِلْءَ الأَرْضِ وَمِلْءَ مَا شِئْتَ مِنْ شَيْءٍ بَعْدُ، أَهْلَ الثَّنَاءِ وَالْمَجْدِ، أَحَقُّ مَا قَالَ الْعَبْدُ، وَكُلُّنَا لَكَ عَبْدٌ، اللَّهُمَّ لاَ مَانِعَ لِمَا أَعْطَيْتَ، وَلاَ مُعْطِيَ لِمَا مَنَعْتَ، وَلاَ يَنْفَعُ ذَا الْجَدِّ مِنْكَ الْجَدُّ".**

❖ "Mil'us Samawati wa Mil'ul Ardi wa Mil'u ma shi'ita min shai'in ba'adu, Ahlus Sana'i wal Majdi, a haƙƙu ma ƙalal abdu, wa Kulluna laka abdun, Allahumma la mani'a lima a'aɗaita, wala mu'uɗiya lima mana'ata wala yanfa'u zal jaddi, minkal jaddu"[64]

## Addu'o'in Sujjada

**سُبْحَانَ رَبِّيَ الأَعْلَى**

❖ "Subhana Rabbiyal A'ala" sau uku[65]

**سُبْحَانَ رَبِّيَ الأَعْلَى وبحمده**

❖ "Subhana Rabbiya A'ala wa bi hamdihi" sau uku.[66]

❖ "Subbuhun Kuddusun Rabbul Mala'ikati war Ruhi"[67]

---

63 Muslim da Abu Awana
64 Muslim da Abu Awana
65 Ahmad
66 Abu Dawud
67 Muslim da Abu Awana

❖ “Subhanakallauhmma Rabbana wa bi hamdika, Allahummagfirli”[68]

**«اللَّهُمَّ لَكَ سَجَدْتُ، وَلَكَ أَسْلَمْتُ، وَبِكَ آمَنْتُ، وَأَنْتَ رَبِّي، سَجَدَ وَجْهِي لِلَّذِي خَلَقَهُ وَشَقَّ سَمْعَهُ وَبَصَرَهُ، تَبَارَكَ اللهُ أَحْسَنَ الْخَالِقِينَ»**

❖ “Allahumma laka sajadtu wa bika amantu wa laka aslamtu, anta rabbi, sajada wajhi lillazi khalaƙahu wa sawwarahu fa ahsana suwarahu wa shaƙƙa sam’ahu wa basarahu, fa tabarakkallu ahasanul khaliƙina ”.[69]

❖ “Allahummagfirli zanbi kullahui diƙƙahu wa jillaha wa awwalahu wa akhirihu wa alaniyyatihu wa sirrihu”.[70]

## Addu’o’in Sallar Dare

**" سُبْحَانَ ذِي الْجَبَرُوتِ وَالْمَلَكُوتِ، وَالْكِبْرِيَاءِ وَالْعَظَمَةِ "**

❖ “Subhana zil jaburiti wal malakuti, wal kibiriya’i wal azamati”.[71]

❖ “Subhanakallahumma wa bi hamdika, la ilaha illah anta”.[72]

❖ “Allahummagfirli ma asrartu wa ma a’alantu”.[73]

---

[68] Bukhari da Muslim
[69] Muslim da Abu Awana
[70] Muslim da Abu Awana
[71] Abu Dawud da Nasa'i
[72] Muslim da Abu Awana
[73] Nasa'i

- ❖ “Allahumma inni a’uzu bi ridhaka min sakaɗika wa bi mu’afatatika min uƙubatik, wa a’uzu bika minka, la uhsi sana’an alaika anta kama asnaita ala nafsika”.[74]

## Addu’o’i Tsakanin Sujjada Biyu

- ❖ “Allahummagfirli warhamni, Wajuburni, warfa’ani, wahdini, Wa'afini, warzuƙni”.[75]

«رَبِّ اغْفِرْلِي، رَبِّ اغْفِرْلِي»

- ❖ “Rabbig firli-Rabbigfirli”, (sau biyu).[76]

## Sigogin Tahiya

Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya koyawa sahabbansa addu’o'i masu yawa daga sigogin tahiya, daga cikinsu:

- ❖ “Attahiyyatu lillahi, wassalawatu waɗɗayyibatu, Assalamu alaika ayyuhan Nabiyyu wa Rahatullahi wa barakatuhu, Assalamu Alaina wa ala ibadullahis Salihina, Ash’hadu alla’ilaha illalahu wa ash’hadu anna muhammadan abduhu wa rasuluhu” Abdullahi ɗan Mas’ud ya kasance yana cewa: “lokacin da Ma’aiki yake raye a cikinmu (haka muke karanta Tahiya) amma bayan rasuwarsa sai muke cewa

---

74 Muslim
75 Abu Dawud da Tirmizi
76 Ibnu Maja

“Assalamu alan Nabiyi (maimakon “Assalamu alaika ayyuhan Nabiyu”).[77]

- “Attahiyyatu aɗɗiyyibatu, assalawatu azzakiyatu lillahi, assalamu alan Nabiyyi wa Rahatullahi wa barakatuhu, assalamu Alaina wa ala ibadullahis Salihina, ash’hadu alla’ilaha illalahu wa ash’hadu anna muhammadan abduhu wa rasuluhu”.[78]
- “Attahiyyatu Mubarakatu, Assalawatuɗ -ɗayyibatu lillahi assalamu alan Nabiyyi wa Rahatullahi wa barakatuhu, assalamu Alaina wa ala ibadullahis Salihina, ash’hadu alla’ilaha illalahu wa ash’hadu anna muhammadan rasulullahi”.[79]

**«التَّحِيَّاتُ لِلّٰهِ، والصَّلَوَاتُ وَالطَّيِّبَاتُ، السَّلاَمُ عَلَيْكَ أَيُّهَا النَّبِيُّ وَرَحْمَةُ اللهِ وَبَرَكَاتُهُ، السَّلاَمُ عَلَيْنَا وَعَلَى عِبَادِ اللهِ الصَّالِحِينَ، أَشْهَدُ أَنْ لاَ إِلَهَ إِلاَّ اللهُ، وَأَشْهَدُ أَنَّ مُحَمَّدًا عَبْدُهُ وَرَسُولُهُ»**

- “Attahiyyatu lillahi, wassalawatu waɗɗayyibatu, assalamu alaika ayyuhan Nabiyyu wa Rahatullahi wa barakatuhu, assalamu Alaina wa ala ibadullahis Salihina, ash’hadu alla’ilaha illalahu wahadahu la sharika lahu, wa ash’hadu anna muhammadan abduhu wa rasuluhu”.[80]

---

[77] Bukhari da Muslim
[78] Ibnu Abi Shaiba da Baihaƙi
[79] Muslim da Abu Awana
[80] Daru Kuɗuni

- “Attahiyyatu aɗɗiyyibatu, wassalawatu liallahi, assalamu alaika ayyuhan Nabiyyu wa Rahatullahi wa barakatuhu, assalamu Alaina wa ala ibadullahis Salihina, ash’hadu alla’ilaha illalahu wa ash’hadu anna muhammadan abduhu wa rasuluhu”.[81]
- “Attahiyyatu lillahi, Azzakiyatu lillahi, aɗɗayibatu lillahi, Assalamu alaika ayyuhan Nabiyu wa Rahmatullahi wa barakatuhu, Assalamu Alaina wa ala ibadillahis Salihina, ash’hadu alla ilaha illallahu, wa ash’hadu anna muhammadan abduhu wa rasuluhu”.[82]

### Sigogin Salatul Ibrahimiyya

**: اللَّهُمَّ صَلِّ عَلَى مُحَمَّدٍ وَعَلَى آلِ مُحَمَّدٍ كَمَا صَلَّيْتَ عَلَى إِبْرَاهِيمَ وَآلِ إِبْرَاهِيمَ إِنَّكَ حَمِيدٌ مَجِيدٌ،**
**اللَّهُمَّ بَارِكْ عَلَى مُحَمَّدٍ وَعَلَى آلِ مُحَمَّدٍ كَمَا بَارَكْتَ عَلَى إِبْرَاهِيمَ وَآلِ إِبْرَاهِيمَ إِنَّكَ حَمِيدٌ مَجِيدٌ ".**

- “Allahumma Salli ala Muhammadin wa ala ali muhammadin kama sallaita ala Ibrahima wa ala ali Ibrahima innaka hamidun Majidun. Allahumma barik ala muhammadin wa ala ali muhammadin kama barakta ala Ibrahima wa ali Ibrahima innaka hamidun majidun”.[83]

---

[81] Muslim da Abu Awana
[82] Malik da Baihaƙi
[83] Bukhari da Muslim

- "Allahumma Salli ala muhammadin wa ala azwajihi wa zurriyyatihi kama sallaita ala ali Ibrahima wa barik ala muhammadin wa ala azwajihi wa zurriyatihi kama barakta ala ali Ibrahima innaka hamidun majidun".[84]
- "Allahumma Salli ala Muhammadin abdika wa rasulika kama sallaita ala ali Ibrahima wa barik ala Muhammadin abdika wa rasulika wa ala ali muhammadin kama barakta ala Ibrahima wa ala ali Ibrahim".[85]
- "Allahumma Salli ala Muhammadin wa ala ali Muhammadin wa barik ala Muhammadin wa ali Muhammadin kama Sallaita wa Barakta ala Ibrahima wa ali Ibrahima innaka hamidun majidun".[86]
- "Allahumma Salli ala Muhammadin Nibiyil Ummiyi wa ala ali Muhammadin kama sallaita ala ali Ibrahima wa barik ala muhammadin nabiyil Ummiyi wa ala ali Muhammadin kama barakta ala ali Ibrahima fil alamaina innaka Hamidun Majidun".[87]
- "Allahumma Salli ala Muhammadin wa ala ahli baitihi wa ala azwajihi wa zurriyatihi kama sallaita ala ali Ibrahim innaka Hamidun Majidun, wa barik ala Muhammdin wa ali baitihi wa ala azwajihi wa

---

[84] Bukhari da Muslim
[85] Bukhari
[86] Nasa'i
[87] Muslim da Abu Awana

zurriyatihi kama barakata ala ali Ibrahima innaka Hamidun Majidun".[88]

## Addu'o'i Kafin Sallama[89]

**اللهُمَّ إِنِّي أَعُوذُ بِكَ مِنْ عَذَابِ جَهَنَّمَ، وَمِنْ عَذَابِ الْقَبْرِ، وَمِنْ فِتْنَةِ الْمَحْيَا وَالْمَمَاتِ، وَمِنْ شَرِّ فِتْنَةِ الْمَسِيحِ الدَّجَّالِ "**

- "Allahumma inni a'uzu bika min azabi Jahannama, wa min azabil Kabari, wa min fitinatil Mahya wal Mamati, wa min Sharri fitnatil Masihid Dajjal".[90]
- "Allahumma inni a'uzu bika min sharri ma amiltu wa min sharri ma lam a'amal ba'adu"[91]
- "Allahummma Hasibni hisaban Yasira".[92]
- "Allahumma bi ilimika gaibi wa ƙuduratika alal khaliƙi ahyini ma alimtal hayata khairan li, wa tawwafani iza kanatil wafatu khairan li. Allahumma wa as'aluka khashyataka fil gaibi wash shahadati wa as'aluka kalimatal haƙƙi wal adli fil gadabi war rida, wa as'alukal ƙasda fil faƙri wal gina, wa as'aluka na'iman la yabidu, wa as'aluka ƙurrata ainin la tanfadu wala tanƙaɗi'u, wa as'alukar rida ba'adal ƙada'i wa as'aluka bardal aishi ba adal mauti, wa as'aluka

---

[88] Ahmad da Ɗahawi
[89] Ana yin su ne bayan kammala tahiya
[90] Muslim
[91] Nasa'i
[92] Ahmad da Hakim

lazzatan nazri ila wajhika, wa as'alukash Shauƙa ila liƙa'ika fi gari darra'a mudirratan wal fitinatan mudillatan. Allahumma zayyinna bi ziniatil Imani, wa ja'alna hudatan muhtadin".[93]

❖ Ma'aiki ya koyawa sayyidina Abubakar faɗin "Allahumma inni zalamtu Nafsi zulman kathira, wala yagfiruz Zunuba illa anta, fagfirli magfiratan min indika warhamni innaka antal gafururrahim".[94]

❖ Haka ya koyawa Nana Aisha faɗin "Allahumma inni as'aluka minal khairi kullihi ajilihi wa ajilihi ma alimtu minhu wa ma lam a'alam, wa a'uzu bika minash Sharri kullihi ajilihi wa ajilihi ma alimtu minhu wa ma lam a'alam wa as'alukal Jannata wa ma ƙarraba ilaiha min ƙaulin au amalin, wa a'uzu bika mina nari wama ƙarraba ilaiha min ƙaulin au amala, wa as'aluka min khairi ma sa'alaka abduka wa rasuluka Muhammadun Sallallahu alaihi wa Sallama, wa a'uzu bika min sharri mas'ta'azaka minhu abduka wa rasuluka Muhammadun Sallallahu alaihi wa Sallama, wa as'aluka ma ƙadaita li min amrin an taj'al aƙibatahu li rushdan".[95]

❖ "Allahumma inni as'aluka Ya Allah! Al wahidul Ahadus-Samadu allazi lam Yalid wa lam Yulad wa

---

[93] Muslim da Abu Awana
[94] Muslim
[95] Abu Dawud da Ibnu Kuzaima

lam yakun lahu kufwan ahadun an tagfirali zunubi, innaka antal gafurur Rahim".[96]

- ❖ "Allahumma inni as'aluka bi anna lakal hamdu la'ilaha illa anta wahadaka lasharika laka al mannanu, Ya Badi'as Samawati wal ardi, Ya zaljalali wal Ikram, Ya hayyu, Ya ƙayyumu, inni as'alukal Jannata wa a'uzu bika minan nari".[97]
- ❖ Ya kasance yana faɗi a ƙarshen tahiyarsa "Allahummagfirli ma ƙaddamtu wa ma akkartu wa ma asrartu wama a'alantu wa ma asraftu wa ma anta a'alamu bihi mini, antal muƙaddimu wa anta mu'akkiru, la'iha illa anta".[98]

## Sallama

- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare ya kasance yana sallama ta ɓangaran damansa yana mai faɗin "Assalamu Alaikum wa Rahmatullahi", yana karkatar da kansa har a ga kuncinsa na dama, haka ma in ya juya ɓangaransa na hagu.[99]
- ❖ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare ya kasance yana cewa "Assalamu Alaikum wa Rahmatullahi wa Barakatuhu" yana karkatar da kansa

---

[96] Nasa'i
[97] Muslim da Ahmad
[98] Muslim da Abu Awana
[99] Muslim

har a ga kuncinsa na dama, haka ma in ya juya ɓangaransa na hagu.[100]

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare ya kasance yana taƙaitawa da faɗin "Assalamu Alaiku wa Rahmatullahi", idan kuma ya juya hagu sai ya ce: "Assalamu Alaikum".[101]

## Addu'o'i Bayan Idar Da Salla

Sigogin "Tasbihi" da "Tahmidi" da "Takbir" da kuma "Hailala" waɗanda suka tabbata guda biyar ne kamar haka:

- "Subhanallahi" sau 33, "Alhamdulillahi" sau 33, "Allahu Akbar" sau 33 da kuma faɗin "La'ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu, lahu mulku, wa lahul hamdu, wa huwa ala kulli shai'in ƙadirun" sau ɗaya.[102]
- "Subhanallahi" sau 33, "Alhamdulillahi" sau 33, "Allahu Akbar" sau 34.[103]
- "Subhanallahi" sau 25, "Alhamdulillahi" sau 25, "Allahu Akbar" sau 25.[104]
- "Subhanallahi" sau 10, "Alhamdulillahi" sau 10, "Allahu Akbar" sau 10.[105]

---

[100] Abu Dawud da Ibnu Kuzaima
[101] Nasa'i
[102] Muslim da Ahmad
[103] Madarijuz Zalimin
[104] Madarijus Salikin
[105] Alwabilus Sail

- “Subhanallahi” sau 11, “Alhamdulillahi” sau 11, “Allahu Akbar” sau 11.[106]

# FASALI NA BIYU:

## WASU DAGA CIKIN HUKUNCE-HUKUNCEN SALLA

[106] Muslim

## ƁANGARE NA FARKO

### Jin Tsoron Allah a Cikin Salla

Allah ya ce: "Haƙiƙa Muminai sun rabauta . Waɗannan da suke jin tsoron Allah a cikin sallarsu".[107] Wato masu jin tsoro ko kuma masu nutsuwa.

### Ma'anar Ƙanƙan Da Kai

Shi ne samun nutsuwa da ƙankan da kai, har hakan ya sanya shi tsoron Allah da kuma kula da umarninsa. Tafsir Ibnu Kathir.

Wato tsayuwar Zuciya a gaban Ubangiji wajen bin Allah da kuma Ƙanƙan da kai.[108]

Gurbin jin tsoron Allah a zuci yake. Maɓuɓɓugarsa kuma jikin gaɓoɓi wanda suke biyayya ga zuciya. Idan jin tsoron Allah ya ɓaci sanadiyyar gafala da wasuwasi; bautar gaɓoɓi ma ta lalace, domin ita zuciya kamar sarki ce, gaɓoɓi kuma kamar runduna ce, da shugaba ake koyi kuma daga gare shi ake karbar umarni, idan sarki ya afka cikin gafala tabbas rundunarsa ta halaka.

Huzaifatul Yaman Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: "Na hane ku da jin tsoron Allah irin na munafukai. Sai aka ce masa, ya jin tsoron Allan Munafukai

---

107 Muslim

108 Bukhari

yake? Sai ya ce: "Shi ne ka ga gangar jiki na jin tsoron Allah amma zuciya ko oho"
Fudailu ɗan Iyad ya ce: "Ana ƙyamatar mutumin da yake bayyana jin tsoron Allah a zahiri fiye da yadda yake a cikin zuciyarsa.
Wani daga cikin magabata ya ga wani mutum a tattakure yana jin tsoron Allah. Sai ya ce: Ya kai wane! Jin tsoron Allah a nan yake (sai ya nuna ƙirjinsa) ba a nan ba (sai ya nuna gabbansa).[109]

## Bambance-Bambancen Mutane Wajen Tsoron Allah (Yayin Salla)

Masu jin tsoron Allah suna da darajoji (mabambanta , shi kuwa jin tsoron Allah aikin zuciya ne, yana ƙaruwa kuma yana raguwa. Daga cikinsu akwai wanda jin tsoron Allan sa yake kai faɗin sama kamar yadda daga cikinsu akwai wanda yake fita daga cikin sallarsa amma bai hankalci komai ba. Mutane suna da darajoji guda biyar a Salla:
Wanda ya zalunci kansa mai sakaci, shi ne wanda ya tauye wasu abubuwa daga cikin alwalarsa da lokutan sallar da iyakokinta da kuma rukunanta.
Wanda ya kiyaye lokutanta da iyakokinta da rukunanta na fili da kuma alwala sai dai bazai iya tanƙwara zuciyarsa wajen hanata Wasiwasi da tunane-tunane.

---

[109] Muslim

wanda yake kiyaye iyakokinta da rukunanta kuma, yana yaƙi da zuciyarsa wajen hanata wasuwasi da tunane-tunane, yana himmatuwa wajen yaƙar maƙiyinsa (Shaiɗan), domin kar ya sace masa sallarsa, irin wannan yana cikin Sallah da kuma Jihadi.

Wanda idan ya shiga Salla yake cika haƙƙoƙinta da rukunanta da iyakokinta, zuciyarsa ta himmatu wajen kiyaye dokokinta da haƙƙoƙinta domin kar ya rasa wani abu daga cikinta, damuwarsa ita ce yinta kamar yadda ya dace, zuciyarsa ta dulmiya cikin lamarin sallarsa da bautar Allah Maɗaukakin sarki a cikinta.

Wanda idan ya tsaya a cikin sallarsa duk gangar jikinsa ma ta tsaya, shi ne wanda yake ɗaukar zuciyarsa kacokan yake sanyata a gaban Ubangiji, yana kallonsa da zuciyarsa, yana kiyaye iyakokinsa, zuciyarsa tana mai cika da ƙaunarsa da kuma ganin girmansa kamar dai yana ganinsa. Ya gusar da dukkan wasuwasi da kuma dukkanin hatsari. Shamaki ya yaye tsakaninsa da Ubanginsa. Wannan tsakaninsa da tsakanin waninsa ne a cikin Sallah shi yafi abin da yake cikin sammai da ƙasa. Irin wannan a cikin sallarsa mai shagala ne da Ubangijnsa, idanuwansa sun yi daɗi.

- ❖ Na farko: Abin hukuntawa ne.
- ❖ Na biyu: Abin bin diddigi ne.
- ❖ Na uku: Abin yafewa ne.
- ❖ Na huɗu: Mai samun lada ne.

- Na biyar: Makusancin Ubangiji ne domin shi yana da wani babban rabo saboda ya sanya jin daɗin idanunsa a cikin sallarsa. Duk wanda idanunsa suka yi sanyi a cikin sallarsa a duniya; tabbas idanunsa za su yi sanyi wajen haɗuwa da Ubangijinsa a Lahira, haka ma a Duniya. Duk wanda idanunsa suka yi sanyi saboda Allah; Dukkanin idanun za su ƙaunace shi. Duk wanda idanunsa ba su yi sanyi saboda Allah ba; asarar duniya ta tabbata a kansa.[110]

## Halayen Masu Jin Tsoron Allah a Cikin Salla

Sayyidina Umar (Allah ya ƙara masa yadda) wata rana yana kan mumbari ya ce: "Ɗayanku zai tsufa a cikin Musulunci ba tare da ya yi cikakkiyar Salla ga Allah ba" sanadiyyar rashin ƙanƙan da kai a cikin sallar kuma ba ya fuskantar Allah mai girma da ɗaukaka"

Wannan faɗin Umar ne a farkon Musulunci; mu kuma yaya halinmu yake a yau!? Da yawa suna cikin wannan halin sai dai wanda Allah ya tsare. Hayaniyar Duniya za ta tafi da jin tsoron Allansa, sai ya zamo yana salla da gangar jikinsa ne amma tunaninsa yana duniya da kasuwanni, duk wannan ya faru ne saboda gafala.

Hasanul Basari ya ce: "Amiru ɗan Abdul Kais ya ji su suna tattaunawa dangane da abin da yake tauye Salla, sai ya ce musu kuna jin haka ne? Sai suka ce ƙwarai ma kuwa. Sai

[110] Al wabil- Sail

ya ce: Kasusuwa su babbake mini a cikin cikina shi yafi soyuwa a gare ni fiye da in samu irin wannan a cikin sallata"

Ya kai ɗan uwana! Me yake damummu ne haka muke bijirewa a cikin Salla, muke tauye wajibin da yake kan mu a kanta, haƙiƙa ɗan Mas'ud idan ya tashi zai yi Salla kai ka ce ratayayyen tufafi ne (Saboda yadda yake kaiwa matuƙa wajen nutsuwa). Sa'idu ɗan Jubair ya kasance idan ya tashi Salla kai ka ce wani sandarrarn tudu ne.

To, ya matsayin sallarmu take in ka haɗamu da waɗancan manyan bayin Allan, wannan Abdullahi ɗan Zubair ne ya kasance idan ya yi ruku'u kai ka ce tsuntsu ne zai sauka a bayansa ba tare da (shi tsuntsun) ya firgita ba. Idan kuwa ya yi sujjada kai ka ce wata tufa ce aka jefar da ita.

Mu a yanzu irin wannan jin tsoron Allan da wannan nutsuwar sun zamar mana wani baƙon abu, ba wani abu ne ya jawo mana haka ba sai dai kasancewar ba ma ganin irin wannan nutsuwar a rayuwarmu ta yau da gobe, in ba haka ba kuwa da bamu samu kan mu a cikin irin wannan rashin jin tsoron Allan ba a cikin Salla. Anbasa ɗan Uƙuba ya kasance idan ya yi sujjada tsuntsaye suna sauka a bayansa kai ka ce a kan busashiyar katanga suka sauka.

Ya kamata mu kasance tare da nagartattun bayin Allah, ga Abubuakar ɗan Ayyash yana cewa: naga Habibu ɗan abi Thabitu yana Sujjada da a ce zaka gan shi a wannan halin

sai ka ɗauka matacce ne saboda yadda yake tsawaita sujjada.
Ibramut Tamimi ya kasance idan ya yi sujjada kai k ace rusassshiyar Katanga ce, tsuntsayen Beni suna sauka a kanta.
Ɗan wahabu ya ce: Na ga Sufyanus Sauri a harami bayan sallar Magriba yana Sallah, da ya yi sujjada bai ɗago daga sujjadar ba har sai da aka kira sallar Isha'i.
Waɗannan magabatan babu wani abin da yake shagaltar da su ga barin Sallah, kuma babu wani abu da yake shiga tsakaninsu da Allah, dukkan tunaninsu ya taƙaita a cikin Sallah haka, suna khushu'i ga Allah kaɗai da kuma ƙasantuwa gaba gare shi.
Imamul Bukhari ya kasance wata rana yana Salla da daddare sai Zuma ta rinƙa harbinsa har sau 17, lokacin da ya idar da sallar sai ya ce, ku duba mini abin da ya cutar da ni.
An karɓo daga Maimun ɗan Hayyanu ya ce: ban taɓa ganin Muslim ɗan Yasar yana waiwaye a cikin salla ba ko sau ɗaya, gajeriya ko doguwa. Wata rana gefen Masallaci ya rushe har mutanen kasuwar da take kusa da masallacin sai da suka razana amma shi yana Salla ko juyawa bai yi ba.
Lokacin da aka tambayi Khalaf ɗan Ayyuba shin ƙudaje ba sa damunka in kana Salla saboda mun lura ba ka koresu. Sai ya ce bana son sabarwa kaina duk wani abu da zai ɓata

mini Salla. Sai aka ce masa ta ya ya kake haƙuri da haka? Sai ya ce musu labari ya zo mani cewa mutanan banza ma suna haƙura da bulalar masu mulki, har ka ji ana cewa wane mai juriya ne, har alfahari suke yi da haka, shin ni da nake tsaye a gaban Ubangijina ta yaya zan yi motsi saboda ƙuda?!

Ɗan Zubair ya kasance idan ya shiga Salla, kai ka ce itace ne (Ya tsaya ƙiƙam) saboda tsoron Allah.

Ƙasim ɗan Muhammad ya ce: Wata rana na yi sammako daman na kasance in zan yi sammako ina biyawa ta wajen Nana Aisha Allah ya ƙara mata yadda don in gaisheta, sai kuwa naje wurinta, sai na tarar tana sallar walaha tana karanta "Famannallahu Alaina…"[111], tana ta kuka, tana addu'a tana maimata ayar, har sai da na ƙosa na tashi amma tana nan yadda take. Da naga haka, sai na yi tafiyata Kasuwa, na ce gwara na je na biya buƙatuna sannan na dawo, bayan na dawo sai na tarar da ita kamar yadda na bar ta.

An tambayi Hatim ɗan Asam game da sallarsa, sai ya ce idan lokacin sallah ya gabato ina kyautata alwala sai nazo wurin da nake so na yi Salla, sai na zauna har sai na samu cikakkiyar nutsuwa sannan na tashi na yi kabbarar Salla ina mai fuskantar alƙibla, ina mai ƙudurce siraɗi ne a ƙarƙashin dugadugaina, Aljanna a damata, Wuta a haguna,

[111] Suratuɗ-ɗur

Mala'ikan Mutuwa yana tsaye a kaina, ina mai ƙudurce wannan ce sallata ta ƙarshe, sannan ina tsaye a tsakanin fatan samun Rahama da tsoron azaba, sannan sai na yi Kabbara ina mai halatto ma'anarta, in kyautata karatu, in yi ruku'u tare da ƙanƙan da kai, in yi sujjada da tsoron Allah, in zauna a kan tafukan ƙafafuna na hagu, in shimfiɗa cikin dugadugaina, in kafe ƙafata ta dama a kan babban ɗan yatsa ina mai tsantsanta niyya ga Allah, sannan ina ƙudurcewa shin Allah ya karɓa ko bai karɓa ba.
Bakar al-muzani ya yi wasiyya game da Salla yana mai kira kan kwaɗaitarwa a kan yin Salla da cikata domin tabbatar da ingancinta, in da yake cewa: "Idan kana son sallarka ta amfane ka; ka ƙudurce a zuciyarka ita ce sallarka ta ƙarshe"
Tare da ba da dukkan cikakkiyar kulawa da Sallah da kuma kiyayeta lallai ɗan Usman ɗan Abi Daharshu ya ce: "Ban taɓa yin wata Salla ba face sai na nemi gafarar Allah saboda taƙaitawata a cikinta"
Ya "Yan uwana! Wallahi wasu irin mutane ne da suka kwatanta abin da aka umarce su da shi, suka yi taka-tsan-tsan wajen jin tsoron zamewa kuma suka nisanci duk abin da zai kaisu ga zamewar, suka kutsa wajen raya dare, suka buɗe litattafansu na zunubi, zuciyarsu ta karye, suka ƙwanƙwasa ƙofar mahaliccinsu suka nemi uzuri sai Allah ya ce "Zan saka muku da abin da kuka yi haƙuri…" sai dai (shin mu ma mun kasance kamar su?!

## Hanyoyin Samuwar Tsoron Allah a Cikin Salla, Da Kuma Abubuwan Da Suke Taimakawa

Ɗan uwana Masallaci! Akwai abubuwa da ake saka rai ta hanyarsu ake kaiwa ga samun tsoron Allah a cikin Salla, waɗannan hanyoyin sun kasu kaso biyu:

Na farko: ba shi da alaƙa da sallar kanta, su ne:

- ❖ Kaɗaita Allah mai girma da ɗaukaka wajen kasantuwarsa Ubnagijin da ya cancanci bauta shi kaɗai, ya kaɗaita wajen ayyukansa, ya kaɗaita cikin sunayensa da siffofinsa.
- ❖ Girmama janibin Ubangiji da kaɗaita bauta a gare Shi da kuma kulawa da haƙƙoƙin Ubangiji cikin abin da ya bayyana da kuma wanda ya ɓuya.
- ❖ Kaɗaita biyayya ga Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi.
- ❖ Jin tsoron Allah ta hanayar aikata abin da ya umarta da kuma barin munanan ayyuka.
- ❖ Cin halal da nisantar Haram da kuma nisantar rikitattun abubuwa (wato abubuwan da suke da ruɗani wajen gane halaccinsu ko haramcinsu)
- ❖ Addu'a da ƙanƙan da kai zuwa ga Allah domin neman ya azurtaka da jin tsoronsa.
- ❖ Kusantar mutanen kirki da kuma rayuwa tare dasu.

Na biyu: waɗanda suke da alaƙa da sallar kai tsaye, su ne:

- Ka tattaro tunaninka kafin fara Salla.
- Jin girman wanda za ka tsaya a gabansa, wato Allah mai girma da ɗaukaka.
- Kwaɗayin samun ladan Salla cikakke.
- Kyautata Alwala da kuma nisantar ɓarnar ruwa da kuma barin lam'a (wofintar wani guri cikin gaɓɓan Alwala).
- Tattaro nutsuwa kafin shiga Salla saboda faɗin Ma'aiki: "Babu Salla idan an kawo abinci ko kuma idan ana danne bahaya ko Fitsari"[112] Kuma gurin sallar ya kasance akwai cikakkiyar nutsuwa.
- Nesantar yiwa sallar riƙon sakainar kashi ta hanyar gabatar da ita tare da Jama'a kuma zuwa Masallaci a kan lokaci (Kafin ko bayan kiran Salla)
- Lazimtar nafiloli musamman waɗanda ake yinsu kafin ko bayan sallolin farilla kamar sallar Wutiri da Rakatanil Fajiri da kuma lazimtar sallar dare.
- Tuntuntuni cikin ma'anonin ayoyin da ake karantawa a cikin Salla da addu'o'in da ake karantawa.
- Nesanatar gaggawa cikin sallar. Kada sallar ta zama ita ce koma baya cikin al'amuranka har ka rinƙa yenta yadda ka ga dama.

[112] Muslim

- ❖ Yin ladabi cikin salla ta hanyar nisantar yawan motsi da waiwaye da wasan da aka hana a cikin Salla.
- ❖ Lazimtar hukunce-hukuncen sallar da ladubanta da kuma sanya ganinka inda za ka yi sujjada. Ma'aiki yana cewa: "Ku yi Salla kamar yadda kuka ganni ina yi"[113]
- ❖ Cikakken koyi da Liman domin shi Liman abin koyi ne a cikin Salla.
- ❖ Ka karkaɗe zuciyarka daga shagalce-shagalcen duniya domin ita duniya gabaɗayanta fitina ce da shagalce-shagalce kuma matsayinta bai kai fiffiken sauro ba a wurin Allah.
- ❖ Nesantar wuraren wasanni da kaɗe-kaɗe da hotuna da ƙyale-ƙyale da jan hankali ko sautuka da kuma yasassun zantuka.
- ❖ Yin sallah irin ta mai ban kwana domin duk waɗanda muka sani sun rasu; sun rasu ne bayan sallar farilla, kai ma haka zata kasance.

Ɗan'uwa Musulmi: Ma'aiki yana cewa: "Babu wani mutum musulmi da sallar farilla za ta gabato ya kyautata alwalarsa da tsoron Allah a cikin sallar da ruku'inta, face ta zamar masa kankarar zunubai mutuƙar bai yi babban zunubi ba, kuma har ƙarshen rayuwarsa"[114]

---

[113] Bukhari
[114] Muslim

Al'amarin jin tsoron wani abu ne mai girma kuma sha'aninsa yana da hatsari, baya samuwa sai ga wanda Allah ya datar da shi, duk wanda aka haramta masa samu tsoron Allah lallai ya haɗu da musiba babba da asara mai girman gaske saboda haka Ma'aiki ya kasance yana faɗi a cikin addu'arsa: "Ya Ubagiji! Ina neman tsarin ka daga zuciyar da ba ta jin tsoron Allah"[115]

Allah ya sanya mana daga cikin ayyuka mafi dacewa, kuma mafi tsarkin niyya akansa, ya sanya mana lada mafi cika da kamala, Ya Ubangiji muna neman tsarinka daga zuciyar da ba ta tsoronka, da idon da ba ya hawaye saboda tsoronka, da addu'ar da ba a amsawa. Ya Ubangiji! Ka yafe mana zunubanmu kuma ka gafart mana mu da iyayenmu da dukkan Musulmi. Amin.

## Kwaɗaitarwa Cikin Al'Amuran Salla

Salla ita ce rukuni na biyu cikin rukunan Musulunci, kuma ita ce mafi girman rukuni bayan Kalmar shahada.

Sallah ita ce ginshiƙin addini, saboda faɗin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "Kan al'amari shi ne Musulunci, Ginshiƙinsa kuma shi ne Salla, kaiwa matuƙarsa shi ne Jihadi".[116]

---

[115] Tirmizi

[116] Tirmizi

Salla ita ce farkon abin da za a fara yi wa bawa Hisabi a kanta ranar Kiyama, idan ta inganta ta kuɓuta sauran al'amura zasu kuɓuta, idan ta samu matsala sauran al'amura duka za su samu matsala kamar yadda Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya bayyana.[117]

Salla ita ce mahaɗa tsakanin bawa da Ubangijinsa, saboda faɗin Ma'aiki: "Idan ɗayanku yana Salla, lallai shi mai ganawa ne da Mahaliccinsa".[118]

Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa, kamar yadda ya zo a cikin Hadisi Kudusi: "Na raba Salla tsakanina da bawana gida biyu, bawana zai samu abin da ya roƙe ni, idan bawa ya ce: "Alhamdulillahi Rabbil Alamina" sai Ubangiji ya ce, "Bawana ya gode mini". Idan bawa ya ce: "Arrahmanir Rahim" sai ubangiji ya ce: "Bawana ya girmamani". Idan bawa ya ce: "Maliki yaumid Dini" sai Ubagiji ya ce: "Bawana ya kambamani". Idan bawa ya ce: "Iyyaka na'abudu wa iyyaka nasta'in" sai Ubangiji ya ce "Wannan tsakanina ne da bawana, kuma zan ba wa bawana abin da ya roƙa" Idan bawa ya ce "Ihdinas Siraɗal Mustaƙim. Siraɗal lazina An'amta alaihim gairil Magdhubi alaihim waladh Dhalina" sai Ubangiji ya ce "Wannan duka na bawana ne, zan kuma ba shi abin da ya roƙa".[119]

---

[117] Tirmizi
[118] Bukhari da Muslim
[119] Muslim

Salla ita ce wasiyyar ƙarshe da Ma'aiki ya yi wa al'ummarsa lokacin da yake kan shimfiɗar rasuwa, kafin a ɗauki ransa zuwa "Rafiƙul A'ala" lokacin da yake cewa: "Ina yi muku wasiyya da tsaida Salla, Ina yi muku wasiyya da tsaida Salla da kuma kiyaye haƙƙoƙin waɗanda suke ƙarƙashinku."[120]

Ɗan'uwa ka zama mai ƙoƙarin kiyaye sallarka domin ita ce bambanci tsakaninmu da waɗanda ba musulmai ba. Kuma ka sani cewa duk wanda ya tsayar da Salla haƙiƙa ya tsayar da Addini, duk wanda ya tozartata, toh ya rushe addini. **Allah Ya kiyaye mu.**

## Kwaɗaitarwa Wajen Tsayar Da Sallolin Farilla Guda Biyar

An karɓo daga ɗan Umar Allah ya ƙara masa yarda, daga Ma'aikin Allah. tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi cewa: "An gina Musulunci a kan abubuwa guda biyar; shaidawa babu abin bautawa da cancanta sai Allah kuma Ma'aiki tsira da amincin Allah ɗan aikensa ne, da tsayar da Salla, da bayar da Zakka, da Aikin Hajj da kuma Azumin Ramadan".[121]

An karɓo daga Abu Huraira Allah ya ƙara masa yarda ya ce Ma'aikin Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Da a ce akwai ƙorama a ƙofar gidan

---

[120] Abu Dawud

[121] Bukhari da Muslim

ɗayanku, kullum yana wanka sau biyar a cikinta, shin wani datti zai rage masa? Kamar haka ne Salloli suke shafe kurakurai".[122]

Usman ɗan Affan Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Ba don wata aya a cikin littafin Allah ba wallahi da ban sanar daku wani Hadisi da naji daga wurin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ba, Ma'aiki yana cewa "Ɗayanku ba zai yi alwala ba kuma ya kyautata alwalar sannan ya yi Salla face sai Allah ya gafarta masa zunubansa dake tsakanin wannan sallar da wacce take biyota".[123]

Usman ɗan Affan Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Na ji Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana cewa: "Babu wani Musulmi da Sallar farilla za ta riske shi kuma ya kyautata alwala da kuma jin tsoron Allah a cikin sallar, da kyautata ruku'inta face wannan sallar ta zamar masa kankarar zunubi ce na abin da yake gabaninta matuƙar bai afkawa manya-manyan laifuka ba, wannan kuwa haka yake har ƙarshen rayuwarsa".[124]

Daga Abu Ayyubal Ansari, Ma'aiki yana cewa: "Salla tana kankare abin da yake tsakanin Salla da Salla na kurakurai".[125]

---

[122] Bukhari da Muslim
[123] Bukhari da Muslim
[124] Muslim
[125] Ahmad

Daga Abu Huraira Allah ya ƙara masa yadda, ya ce: Ma'aiki ya ce: "Mala'ikun dare da na Rana suna canjin aiki a tsakaninsu, suna haɗuwa a sallar Asubahi da kuma Sallar La'asar. Idan Mala'ikun dare suka koma zuwa sama sai Ubangiji ya tambayesu alhalin ya fisu sani, yaya kuka baro bayina? Sai su ce, mun bar su suna Salla, kuma lokacin da muka je mun same su suna Salla".[126]

An karɓo daga Ubada ɗan Samitu Allah ya ƙara masa yadda ya ce: Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Sallaloli biyar allah ya wajabtawa bayinsa duk wanda yazo da su ba tare da ya tozarta wani abu daga cikinta ba saboda raini yana da alƙawari tsakaninsa da Ubangiji cewa zai shigar da shi Aljanna. Duk wanda bai zo da su ba, ba shi da wani alƙawari tsakaninsa da Ubangiji, in yaso ya yi masa Azaba in kuma yaso ya shigar da shi Aljanna".[127]

An karɓo daga Anas Allah ya ƙara masa yadda y ace: Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Farkon abin da za a yi wa bawa Hisabi a kai ranar Alƙiyama ita ce Salla, idan ta yi kyau haƙiƙa ya rabauta, idan ta ɓaci haƙiƙa ya taɓe ya yi asara".[128]

A wata ruwayar kuma farkon abin da za a yi wa bawa hisabi ranar ƙiyama shi ne Salla, idan ta inganta ragowar

[126] Bukhari da Muslim
[127] Abu Dawud
[128] Ɗabarani

ayyukansa ma sun inganta. Idan ta ɓaci ragowar ayyukansa ma sun ɓaci.

An karɓo daga Ammar ɗan Yasir Allah ya ƙara masa yadda ya ce: na ji Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana cewa: "Lallai bawa zai Sallaci sallar da aka wajabta masa ba zai samu komai a cikinta ba sai ɗaya bisa goma ko ɗaya bisa tara, ko ɗaya bisa takwas, ko ɗaya bisa bakwai, ko ɗaya bisa shida, ko ɗaya bisa biyar, ko ɗaya bisa huɗu, ko ɗaya bisa uku, ko ma rabinta".[129]

## Wajabcin Salla a Cikin Jama'a

Dalilai da suke nuni zuwa ga wajibcin salla a cikin Jama'a daga Kur'ani da sunnar Ma'aiki da kuma maganganun Sahabbai suna da yawa sosai, kuma basa ɓuya ga mafi yawan mutane, don haka za mu taƙaita a kan ambaton wasu da za su zama hujja.

## Dalilai Daga Kur'Ani

❖ Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: "Kuma ku tsayar da Sallah Ku ba da Zakka, kuma Ku yi Ruku'u tare da masu yin Ruku'u"[130]. Faɗinsa Maɗaukakin Sarki "Ku yi Ruku'u tare da masu yin Ruku'u" wannan yana nuni zuwa ga wajabcin sallar Jama'a, da kuma halartar sallarsu. Da yin sallar kaɗai ake nufi da faɗinsa

[129] Abu Dawud da Baihaƙi, da Ahmad da Ibnu Hibban
[130] Baƙara

Maɗaukakin sarki "Ku tsayar da Salla" kaɗai ya wadatar.

- ❖ Allah Maɗaukakin sarki ya ce: "Kuma idan ka kasance a cikinsu, sai ka tsayar musu da Sallah, wata ƙungiya daga gare su ta tsaya tare da kai".[131] Abin lura a cikin ayar, har a lokacin yaƙi Allah ya wajabta sallar Jama'a lallai a halin zaman lafiya kuwa ita tafi cancanta a tsayar da ita. Da akwai waɗanda za a yafewa sallar Jama'a lalle da su ne waɗanda suke fuskantar maƙiya Allah a filin daga, wanda suke cikin fargabar kowane lokaci za a iya kawo musu farmaki, lallai su ne suka fi cancanta da a yafe masu.
- ❖ Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: "Ranar da za a yaye ƙwari kuma a kira su zuwa ga yin sujjada amma ba za su iya ba (43) Su fito da Idanu ƙasƙantattu, wulaƙanci ya rufe su, lallai ne su a baya sun kasance ana kiransu zuwa ga sujjada alhalin kuwa suna lafiya ƙalau (amma suka ƙi yi)".[132]
- ❖ Sa'idu ɗan Musayyib ya ce: "Sun kasance suna jin ana cewa "Ku taho zuwa ga Salla, Ku taho zuwa ga rabauta" ba sa amsawa alhalin lafiyarsu ƙalau, ba su da wani uzuri" .

[131] Nisa'i
[132] Kalam

❖ Ka'abul Ahbar ya ce: "Wallahi wannan ayar bata sauka ba face a kan wanɗanda ba sa zuwa sallar jama'a"

❖ Yanzu akwai narkon azabar da yafi wannan muni a kan wanda yake da ikon zuwa sallar Jama'a amma baya zuwa?!

## Koyarwar Ma'Aiki

❖ An karɓo daga Abu Huraira Allah ya ƙara masa yarda, Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Wallahi na himmatu in ba da umarnin a fara Salla, sai na umarci wani ya yi Limanci sannan na tafi tare da wasu mutane ɗauke da itatuwa domin mu babbake gidajen waɗanda ba sa zuwa sallar Jama'a"[133]. Tabbas Ma'aiki ba zai umarnin ƙone gidaje ba face a kan barin abin da yake wajibi ne.

❖ An karɓo daga ɗan Abbas Allah ya ƙara masa yadda, Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Duk wanda ya ji mai kiran Salla yana kiran Salla kuma babu wani uzuri da ya hana ya amsa masa, face ba za a karɓi wannan sallar tasa ba. Suka ce mene ne uzurin ya Ma'aikin Allah. Sai ya ce: "Tsoro da rashin lafiya".[134]

---

[133] Bukhari da Muslim
[134] Abu Dawud da Ibnu Hibban da Ibnu Maja

## Daga Cikin Maganganun Sahabbai

- Abdullahi ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda ya ce: "Duk wanda yake so ya haɗu da Allah ranar Alƙiyama ,to, ya kiyaye salloli guda biyar duk lokacin da ya ji an kirasu. Lallai Ubangijinku ya shar'antawa mazanaku hanyoyi na shiriya, kuma salloli biyar a cikin Jama'a suna daga cikinsu, da za ku yi sallolin a cikin gidajenku kamar yadda waɗanda suka suke yi lallai da kun bar shiriyar Annabinku. Idan kuma ku kabar shiriyar Annabinku; tabbas kun ɓata. Babu wani ɗaya da zai yi alwala kuma ya kyautata alwalarsa, sannan ya tafi ɗaya daga cikin waɗannan masallatan face Allah ya rubuta masa duk taku ɗaya kyakkyawa ɗaya, ya ɗaukaka darajarsa da shi kuma ya kankare masa zunubansa da shi. lokacin da na kallemu (taron Sahabbai) sai naga babu wanda yake ƙin halattar sallar jama'a sai dai munafuki, wanda aka san shi akan munafurcin. Kuma an kasance ana zuwa da mutum ya tsaya a tsakanin mutane biyu har sahu ya tsaya"
- **Aliyu ɗan abi Ɗalib** ya ce: "Babu Salla ga maƙocin Masallaci sai dai in a cikin masallacin ya yi. Suka ce wane ne maƙocin masallaci? Ya ce: duk wanda yake jin kiran sallar masallacin".[135]

---

[135] Ahmad

- **Abu Huraira** ya ce: “Alburusai su cika kunnan ɗan'adam shi yafi masa alheri a kan yana jin ana kiransa zuwa Salla amma bai amsa ba”
- Bayan waɗannan bayyanannun hujjojin shin akwai wani uzuri da ya ragewa wanda ba ya zuwa sallar jama’a!? wannan hujjane a kan duk wanda ya karanta ko ya saurara domin a kan su za a yi masa hisabi ranar Alƙiyama. Allah shi ne majiɓancin masu dace.

## Fa’idojin Salla a Cikin Jama’a

- Ubangiji ya shar’anta sallar Jama’a saboda wata hikima mai girma da kuma falaloli masu tarin yawa, daga ciki:
- Jarraba bayi da kuma gwadasu domin sanin mai biyayya ga umarnin Allah da kuma mai saɓa masa.
- Samar da haɗin kai da ƙara danƙon soyayya da ƙulla kyakkyawar mu’amala tsakanin musulmai domin su zama kamar gangar jiki guda ɗaya, kamar gini da sashinsa yake ƙarfafar sashi. Duk wanda ba ya salla a cikin jama’a ba zai san mutanen unguwarsu ba, kuma babu wani da zai yi mu’amala da shi, sai wanda wata maslahar duniya ta haɗa su.
- Koyar da Jahili da kuma tunatar da rafkananne. Jahili zai ga mai ilimi sai ya yi koyi da shi. rafkananne zai saurari faɗakarwa sai ya amfana da ita.

- ❖ Mai salla a cikin jama'a yana samu jin tsoron Allah da nazari cikin ma'anar ayoyin da ake karantawa, saɓanin wanda yake salla a gida shi kaɗai. Mafi yawan lokaci mai Salla shi kaɗai gundurarsa take, nan da nan sai ya sallame.
- ❖ Cusa baƙin ciki a zukatan maƙiya Allah da kuma samun kwarjini a idanunsu musamman shaiɗan da rundunarsa da bijirarrun aljanu, wanda zuwa Masallaci yake ɓata musu rai, musamman idan suka ga samari suna Salla.
- ❖ Fita zuwa Masallaci yana zama kamar motsa jiki ga mai Salla, kuma yana ƙara masa nishaɗi da lafiya musamman idan masallacin yana da 'yar tazara. Wannan duk saɓanin wanda ya yi salla a gida.
- ❖ Wannan kaɗan ne daga cikin fa'idojin sallah a Masallaci a cikin jama'a, ko shakka babu akwai wasu fa'idojin masu yawa daban, don haka ɗan'uwa ka kiyaye yin sallah a cikin jama'a don ka samu kuɓuta daga munafurci.
- ❖ Anas ɗan Malik Allah ya ƙara masa yarda ya ce, Ma'aiki ya ce: "Duk wanda ya yi sallar kwana arba'in a cikin mutane yana mai riskar kabbarar harama za a rubuta masa kuɓuta biyu; kuɓuta daga wuta da kuma kuɓuta daga munafurci".[136]

[136] Tirmizi

## Narkon Azaba Ga Wanda Ya Bar Sallar Jama'a Ba Tare Da Uzuri Ba

- ❖ An karɓo daga ɗan Abbas Allah ya ƙara masa yarda, Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Duk wanda ya ji kiran Sallah amma bai amsa ba, ba shi da Salla sai da uzuri".[137]
- ❖ **Abdullahi ɗan Mas'ud** ya ce: "Da a ce za ku yi sallarku a cikin gidajenku kamar yadda wancan da ya saɓa yake yi; tabbas da kun bar koyarwar Annabinku, in kuwa kuka bar koyarwar Annabinku lallai kun halaka"
- ❖ An karɓo daga Abu Huraira Allah ya ƙara masa yarda, wani mutum makaho ya zo wurin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: Ya Ma'aikin Allah! Bani da ɗan jagora da zai kaini zuwa Masallaci, sai ya roƙi Ma'aiki ya yi masa rangwaman zuwa sallar jam'i. Sai Ma'aiki ya yi masa rangwaman. Bayan ya juya sai Ma'aiki ya kira shi ya ce: "Kana jin kiran Sallah"? Makaho ya ce: E! Sai Ma'aiki ya ce masa: Ka amsa.[138]
- ❖ An karɓo daga **Abu Huraira** Allah ya ƙara masa yarda, Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Wallahi na himmatu in ba da umarnin a fara Salla, sai na umarci wani ya yi Limanci sa'annan na

---

[137] Ibnu Maja da Ibnu Hibban
[138] Muslim

tafi tare da wasu mutane ɗauke da itatuwa domin mu babbake gidajen waɗanda ba sa zuwa sallar Jama'a"

- ❖ Daga Abu Burdata daga mahaifinsa Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Duk wanda ya ji kiran Salla yana lafiyayye, ba da wani uzuri ba sannan bai amsa ba; ba shi da Salla.

### Tambayoyi Dangane Da Wajabcin Sallar Jama'a

TAMBAYA: Da yawa daga cikin musulmai suna sakaci wajen gabatar da Salla a cikin Jama'a har da wasu ɗaliban ilimi, kuma suna kafa hujja da cewa wasu malaman sun ce ba wajibi ba ne (yin) salla a cikin jama'a, mene ne hukuncin sallar (yin salla a cikin) Jam'i? Kuma wace irin nasiha za a yi wa yan'uwa?

AMSA: Ko shakka babu Salla a Masallaci kuma a cikin Jama'a tilas ce a bisa mafi kyau kuma mafi rinjayen maganganun malamai a kan dukkan wani Musulmi baligi da ya ji kiran Salla, kuma yana da ikon zuwa saboda faɗin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "Duk wanda ya ji kiran Salla amma bai amsa ba; ba shi da Salla sai dai in da uzuri"

TAMBAYA: Wani lokacin ina dawowa gida a gajiye, a wahale, ina kwanciya barci a makare, hakan ya sanya sallar

Asuba a jam’i take mini wahala, sai dai na yi a gida, shin hakan ya halatta?

AMSA: abin da yake tilas a kan musulmi shi ne ya yi dukkanin salloli guda biyar tare da yan'uwansa a cikin jam’i. Ba ya halatta ya yi raki har ya bar salla a cikin jama’a ko kuma ya rinƙa yinta a cikin kasala domin hakan yana daga cikin siffofin munafukai kamar yadda Ubangiji ya bayyana a cikin suratut Nisa’i.

## SALLAR MUTUM ƊAYA A BAYAN SAHU

Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: “Babu Salla ga mutum shi kaɗai a bayan sahu”.[139]

Malamai sun yi saɓani dangane da sallar mutum ɗaya a bayan sahu:

- ❖ Sallarsa ta yi amma kuma ladan ya tawaya, kamar yadda Ma’aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya faɗa: “Babu Salla idan aka kawo abinci” wannan kuma shi ne maganar Limamai guda huɗu.
- ❖ Sallarsa ɓatacciya ce, bata ingantaba ta kowanne hali, ko da kuwa sahu ne ya cika ya yi Salla shi kaɗai.

[139] Ahmad da Ibnu Maja

Wannan shi ne abin da yafi shahara a mazahabin Imamu Ahmad ɗan Hanbal.

- Ibnu Taimiyya ya shiga tsakani ya ce: Idan sahu ya cika, to, ya halatta mutum ya yi Salla shi kaɗai a sahun baya, domin ba zai iya samun sahu ba, kuma Allah ba ya ɗaurawa rai wani abu face abin da zai iya. In kuwa sahu bai cika ba; ba ya halatta ya yi salla a sahun baya domin ba shi da uzuri.

A Taƙaice

Shaikh ɗan Usaimin ya ce: Idan sahu ya cika, to, ka fara sabo kar ka jawo kowa, kar ka gabaci Liman, wannan shi ne abin da muke ganin yafi kyau fiye da wanda ya ce taɓaci gabaɗaya ko kuma wanda ya ce ta inganta gabaɗaya.

## Hukuncin Wanda Ya Bar Salla

- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Tsakanin mutum da shirka da kafirci shi ne barin Salla".[140]
- Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Alƙawarin da yake tsakaninmu da su shi ne Salla, duk wanda ya bar ta ya kafurta".[141]
- Dukkanin malamai sun haɗu akan kafircin duk wanda ya bar Salla yana mai inkarin wajibcinta, amma sun yi saɓani dangane da wanda ya bar ta saboda kasala:

[140] Muslim
[141] Ahmad da Tirmizi

- ❖ Wasu malaman suka ce ya kafirta, kafirci mai fitar da mutum daga tafarki, ya bar sallar saboda ya yi musun wajibcinta ko saboda kasala saboda gamewar Hadisin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi da ya ce: "Tsakanin mutum da shirka da kafirci shi ne barin Salla"
- ❖ Wasu sun tafi akan wanda ya bar sallah saboda kasala to shi bai kafirta ba kafircin da zai iya fitar da shi daga tafarki, abin sani dai fasiƙi ne, kuma sun kafa hujja da Hadisin Biɗaƙa.
- ❖ Abin da yafi shi ne maganar Ibnu Taimiyya da yake cewa a cikin Al-Fatawa cikin mas'alar wanda yake sallah wani lokacin kuma wani lokacin ya ƙyaleta, sai ya ce: "Mafi yawa daga cikin mutane ba sa kiyaye sallolin farilla, kuma su ba sa daga cikin masu barin sallar gabaɗaya (masu wasa da lokacin salla) irin waɗannan akai \imani da Munafurci a cikin zuciyarsu, hukunce-hukuncen Musulunci duk za su tabbata a kan su a zahiri kamar dai yadda ya kasance yana gudana a kan ɗan Salul"
- ❖ Ya sake faɗa a wani gurin daban a cikin Fatawa: wanda ya kasance ba ya Salla kwatakwata kuma ya mutu akan haka, wannan bai zama daga cikin musulmai ba, tare da cewa mutane da yawa suna yin Sallah wani lokacin kuma ba sa yi, waɗannan basu

zama daga cikin masu kiyaye Salla ba, irin wannan suna cikin wani narkon azaba, irinsu ne Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake cewa akansu: "Salloli guda biyar Allah ya wajabtawa bayinsa a cikin dare da yini duk wanda ya kiyaye su yana da alƙawarin Allah zai shigar da shi Aljanna, duk wanda bai kiyaye su ba; bashi da wani alƙawari a wajen Allah, in yaso ya azabtar da shi, in yaso ya yi masa gafara".[142]

- ❖ Wanda yake Salla akan lokacin da Allah ya sanya shi ne mai kiyaye Salla, wanda kuma yake wasa da lokutanta da kuma yinta yana ƙarƙashin ganin damar Ubangiji, (in yaso ya yi masa gafara in yaso ya azabtar da shi), wataƙila yana da wasu nafiloli da za a cika abin da ya bari na farilla.
- ❖ Sheikh Abdul'Aziz bn Baz ya ce; "Idan ya tabbata wanda ya bar Salla ya kafirta, kafirci na ridda to wannan hukuncin waɗanda suka yi ridda ne yake hawa kansa, daga cikinsu:
- ❖ Ba zai aurar ba (Walicci ko wakilci) kuma ba za a aura masa, in kuwa aka aura masa auran ya lalace.
- ❖ Idan ya bar sallar ne bayan an ɗaura masa aure; wannan auran za a raba shi ne.
- ❖ Idan ya yi yanka ba za a ci ba.

[142] Abu Dawud

- ❖ Ba ya halatta ya shiga garin Makka da iyakokinta
- ❖ Idan makusancinsa ya mutu ba zai ci gado ba.
- ❖ Idan ya mutu ba za a yi masa wanka ba, ba za a sanya masa likkafani ba, ba za a yi masa Salla ba, ba za a bin ne shi a maƙabartar musulmai ba, za a fitar da shi zuwa sahara a yi rami a binne shi a cikin tufafin da ya rasu domin ba shi da wata alfarma
- ❖ Za a tashe shi tare da Fir'auna da Hamana da Karuna da Ubayyu ɗan Khalaf –shugabannin Kafirai, Allah ya tsare mu- ba zai shiga Aljanna ba, kuma ba ya halatta ga ɗaya daga cikin danginsa su roƙa masa Rahma da gafara domin shi Kafiri ne bai cancanci a roƙa masa ba, saboda faɗinsa Maɗaukakin Sarki: "Ba ya kasancewa ga wani Annabi da waɗanda suka yi imani da su nemawa mushirikai gafara ko da sun kasance daga cikin makusantansu ne bayan ya bayyana a gare su cewa su yan wuta ne".[143]
- ❖ Yan'uwa! Lamarin mai girma ne kuma mai hatsarin gaske, abin taƙaici za ka ga mutane da yawa suna sakaci a cikin wannan al'amarin, har a rinƙa zama da wanda ba ya Salla a gida ɗaya, wannan ba ya halatta. **Allah ne mafi sani.**

---

[143] Tauba

## SIFFOFIN SALLAR MA'AIKI (S.A.W)

Daga Abdul'Aziz bin Baz zuwa ga duk wanda yake so ya yi Salla kamar yadda Ma'aiki ya yi, ya yi koyi da faɗinsa: "Ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi", Ma'aiki ya kasance yana Salla kamar haka, kuma mu ma yana da kyau mu kwatanta:

- Ya kyautata alwala kuma ya cikata.
- Ya nufi wurin Salla ya fuskanci alƙibla.
- Ya yi kabbarar harama "Allahu Akbar"
- Ya ɗaga hannunsa ya zuwa kafaɗunsa ko kuma daura da kunnuwansa.
- Ya ɗaura hannunsa na dama akan na hagu a ƙirjinsa.
- An so ya karanta addu'ar buɗe Salla, "Allahumma ba'id baini wa baina khaɗayaya kama ba'atta bainal mashriƙi wal magribi. Allahumma naƙƙini min

khaɗayaya kama yunaƙƙa saubul abyadhu minaddanasi. Allahummagsilni min khaɗayaya bil ma'i wa salji wal baradi"

- Ko kuma ya ce: "Subhanakallahumma wa bi hamdika wa tabarakasmuka, wa ta'ala jadduka, ala ilaha gairuka"
- Sannan ya ce: "A'uzubillahi minash shaiɗanir Rajim, Bismillahir Rahminir Rahim". Ya karanta suratul Fatiha, ya faɗi "Amin" a ƙarshen Fatiha a bayyane a cikin sallar da ake bayyana karatu sannan ya karanta abin da ya sawwaƙa daga cikin surori.
- Sannan ya yi ruku'u yana Kabbara yana mai ɗaga hannuwansa har zuwa kafaɗunsa ko kuma daura da kunnuwansa, yana saita kansa da gadon bayansa, yana mai shimfiɗa hannuwansa akan cinyoyinsa, yana mai rarrabe 'yan yatsunsa, a tsanake yana cewa "Subhana Rabbiyal Azim"
- Ya ɗago kansa daga ruku'u.
- Ya tafi sujjada yana mai kabbara, yana fara gabatar da gwiwoyinsa kafin tafukan hannayensa (Idan yana da ikon yin hakan), ya yi sujjada a kan gaɓoɓi guda bakwai, yana faɗin "Subhana Rabbiyal A'ala"
- Ya ɗago kansa yana mai kabbara.
- Ya yi sujjada ta biyu yana mai kabbara.
- Ya ɗago kansa yana mai kabbara.

- Idan sallar mai raka'a biyu ce; zai zauna bayan ya ɗago daga sujjada yana mai toge ƙafarsa ta dama, yana mai shimfiɗa ta hagun, yana mai sanya hannunsa na dama akan cinyarsa ta dama, yana damƙe yatsunsa gaba ɗaya amma ban da na nuni, yana nuni zuwa kaɗaituwar Allah tare da ambatonsa a lokacin addu'a.
- Idan sallar mai raka'a uku ce kamar Magariba ko kuma mai raka'o'i huɗu ce kamar Azahar da La'asar da kuma Isha'i, to zai karanta Tahiya tare da yi wa Annabi Salati, sannan ya miƙe yana mai dogara akan ƙafarsa, yana mai ɗaga hannuwansa daura da kafaɗunsa yana faɗin "Allahu Akbar" ya sanya hannuwansa akan ƙirjinsa ya karanta Fatiha.

## Addu'o'i Bayan Idar Da Sallah

Daga Abdul'Aziz bn Baz zuwa ga ɗaukacin musulmai, yana daga cikin koyi da Ma'aiki duk wani musulmi ya faɗa bayan idar da Salla:

**أَسْتَغْفِرُ اللهَّ**

- *"Astagfirullah" sau uku.*

**«لاَ إِلَـهَ إِلاَّ اللهُ وَحْدَهُ لاَ شَرِيكَ لَـهُ، لَـهُ الْمُلْكُ وَلَـهُ الْحَمْدُ وَهُوَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ، لاَ حَوْلَ وَلاَ قُوَّةَ إِلاَّ بِاللهِ، لاَ إِلَـهَ إِلاَّ اللهُ، وَلاَ نَعْبُدُ إِلاَّ إِيَّاهُ، لَـهُ النِّعْمَةُ وَلَـهُ الْفَضْلُ، وَلَـهُ الثَّنَاءُ الْحَسَنُ، لاَ إِلَـهَ إِلاَّ اللهُ مُخْلِصِينَ لَـهُ الدِّينَ وَلَوْ كَرِهَ الْكَافِرُونَ»**

- *"La'ilaha illal Lahu wahdahu la sharika lahu, lahul mulku wa lahul hamdu wa huwa ala kulli shai'in ƙadir. La haula wala ƙuwwata illa billahi, la'ilaha illal laha, wala na'abudu illa iyyahu, lahun ni'imatu wa lahul fadhlu, wa lahus sana'ul hasan. La'ila illal laha, mukhlisina lahuddina walau karihal kafiruna. Allahumma la mani'a lima a'aɗaita wala mu'uɗi'a lima mana'ata wala yan fa'au zal jaddi minkal jaddi"*
- Ya faɗa bayan sallar Magrib da sallar Isha'i (bayan addu'I'n da suka gabata): "La'ilaha illal lahu, wahdahu la sharika lahu, lahul mulku wa lahul hamdu, yuhuyi wa yumitu, wa huwa ala kulli sha'in ƙadir" sau goma.
- Sannan faɗi bayan haka "Subhannallahi" sau 33, "Wal Hamdulillahi" sau 33, "Wallahu Akbar" sau 33. Ya faɗa a cikon na ɗari "La'ilaha illal lahu wahdahu la sharika lahu lahul mulku wa lahul hamdu wa huwa ala kulli shai'in ƙadir."
- Sannan ya karanta Ayatul Kursiyu.
- Sannan ya karanta suratul Ikhlas da Falaƙi-da-Nasi. Bayan sallar Magrib da Asubahi ya karanta su sau uku, shi yafi falala.

## Tambayoyi Masu Muhimmanci

- Hukuncin ƙarin adadin tasbihi a ruku'u da sujjada?

Sheikh bin Baz ya ce: Babu laifi a yi sau uku ko biyar ko kuma bakwai in ya ƙara suka kai tara ko goma shi ne abin da yafi a cikin ruku'u da sujjada.[144]

- **Shin "Basmala" aya ce daga cikin ayoyin Fatiha ko kuma, aya ce mai zaman kanta?**

Aya ce mai zaman kanta, ba ta daga cikin Fatiha.

- **Shin zai yi "Isti'aza" a kowace raka'a ko kuwa a ta farko kaɗai?**

Bin Baz ya ce: "Wanda ya nemi tsari bai yi laifi ba, wanda ya barta a ragowar raka'o'i babu laifi, amma ko shakka babu zuwa da ita a raka'ar farko yana da matuƙar muhimmanci".

Bin Usaimin ya ce: "Zai nemi tsari ne kaɗai a raka'ar farko domin karatun Salla gabaɗayansa karatu ɗaya ne, sai dai in bai yi ta ba, kamar wanda ya samu Liman a raka'a ta biyu to zai zo da ita. Lamari da sha'anin neman tsari a cikin kowace raka'a abu ne mai yalwar gaske."

- **Shin (yayin )kabbara kansa kaɗai zai jiyar ko kuwa motsawar harshe da leɓe sun wadatar?**

Bin Baz ya ce: "Babu makawa sai ya jiyar da kansa kuma harshensa da leɓansa sai sun motsa"

[144] Fatawa Nurul ala Dharab

Bin Usaimin ya ce: “Ba dole ne ya jiyar da kansa ba, kawai ya wadatar masa ya motsa harshensa da lebansa”

Na ce: Motsa leɓe da harshe wajen karatu da ambaton Allah wajibi ne, saɓanin na jiyarwa, amma ƙudurcewa a zuciya kaɗai bai wadatar ba.

- **Shin liman yana shiru bayan karatun Fatiha?**

Bin Baz ya ce: “Shiru biyu ne ya tabbata a cikin Hadisi. Na ɗaya bayan kabbarar harama kafin fara karatun Fatiha. Na biyu bayan kammala karatun Sura kafin Ruku’u domin rarrabewa tsakanin karatun Salla da kuma tafiya ruku’u. Sannan an rawaito wani shirun na uku; bayan kammala Fatiha sai dai Hadisin yana da rauni. Babu wani dalili tabbatace a kan hakan, abin da yafi shi ne barinsa. Amma a ce bidi’a ne hakan bai dace ba saboda saɓani ne sanan ne a tsakanin ma’abota ilimi.[145]

---

[145] Majmu'ul Fatawa 11/84

## Kammalawa

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah mai cikakken sani da kuma hikima, wanda ya datar da mabuƙacin bawansa domin rubuta wannan taƙaitacciyyar nasiha. Gare shi dukkan yabo da godiya adadin halittarsa da yardar zatinsa da nauyin al'arshinsa da mamakon kalmominsa suke tabbata. Sannan kuma ina godiya ga dukkanin wanda ya taimake ni, ya sanar da ni wani abu cikin rubuta wannan nasihar.

Ba na da'awar wannan yar taƙaitacciyar nasihar da na sanya wa suna "At-Tanwi'u fi Azkaris Salati" wani ƙoƙari ne na musamman daga gare ni, sai dai zan faɗi kamar yadda babban malami as-Sa'adi ya faɗa: "Wannan wasu fa'idoji ne da na tattaro su daga litattafan malamai, Allah

ya saka musu da mafificin alheri kuma ya yi musu gafara, ya yafe musu kuma ya basu babban rabo."
Ina roƙon Allah mai girma da ɗaukaka da sunayensa kyawawa da siffofinsa Maɗaukaka da ya karɓi wannan aikin kuma ya sanya shi mai amfani kuma mai amfanarwa a gare ni da kuma yan'uwana Musulmai. Ya yafe mani duk abin da ya faru na kuskure a cikin rubutun domin shi mai ji ne kuma mai amsawa ne.
Ya Allah ka yi daɗin tsira da albarka ga bawanka kuma manzonka Ma'aiki ɗan Abdullahi da iyalan gidansa da abokansa da waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa izuwa ranar sakamako.
Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin Halittu.
Ɗariƙu ɗan Muhammad Al-Kaɗɗan.
t.ƙatten@gmail.com

## Wasu Cikin Litattfan Marubucin da Aka Buga

1. Wasu Daga Cikin Halayen Magabata (من أخلاق السلف)
2. Fayyataccen Bayani a Kan Siffar Sallar Annabi (S.A.W) Da Kurakuran Masallata
3. Fassarar  Littafin Ahlari Da Sharshi

## Wasu Litattafan Mawallafin Da Suke Tafe

1. Haƙiƙanin Jana'Iza a Musulunci Da Kurakuranta
2. Rayuwar Aure a Musulunci Da Kurakuranta
3. Kasuwanci a Musulunci
4. Riba Da Illolinta
5. Tsarin Da'awa a Musulunci Da Kurakuransa
6. Hanyoyin Cin Nasara a Rayuwa
7. Fassarar Littafin Ta'alimul Muta'allim

8. Usulul-Iman Wa Samaratuhu أصُول الإيمان وثمراته للمعاهد والكليات

9. Siyasa a Musulunci Da Amfaninta.

Ana maraba da dukkanin wani gyara ko shawara mai kyau, ga mai buƙatar ɗaukar nauyin buga ɗaya daga cikin waɗannan litattafai, ko gabaɗaya; sai a tuntuɓi cibiyar fassara ta Ar-Rayhan:

GSM: 08036223067s

Whatsapp: 07049325138

Email: abuamatullahi83@gmail.com